*NAKASA BAKASAWA BACE*

Part 3

Www.kanopost.ng

: Yana surutai, sai dai jin mgnar tashi a wani irin gigice.
tana son ta saita nitsuwarta ta tabbatar wa kanta abinda takeji amman ina sai take jin abin a bai-bai

Sama da 50 minute suka ɗauka suna abu ɗaya, gaba ɗaya sun gigice, duk wani tunaninsu ya kau, wannan daren yakasance musu wani dare na mussaman, dan kuwa sun shayar da junansu, zuman soyayya, surutai da sambatu kuwa babu irin wanda basu yi ba sun nuwa juna asalin soyayyar da sukewa junansu.
Ahankali ya kwanta ajikinta, yana sakin wani irin ƙaƙƙarfan ajiyar zuciya, kusan atare suke fitar da numfashi, gaba ɗaya tayi laushi, dan ya mugun gajiyar da ita ƙwarai, saidai kuma zaƙin daya shayar da ita, bazai faɗu ba, dan har yanzu awata duniya ta daban takejin kanta.

Kissing goshinta yayi, cikin zuciyarsa yace. "Allah Ya miki Albarka my shugar na, tabbas keɗin ta dabance acikin mata, ni'imarki daban take, komai naki is perfect, I love you with all my heart."
Ɗan mirginawa gefenta yayi, hannunsa yasa yaɗan riƙe bayansa dake masa ciwo, dan yayi mugun gajiya, wanda sai ayanzu ne kuma yakejin gajiyan, sabanin ɗazu dayake ta kwasan garaɓasa baiji gajiyan ba. Kusan mintuna goma suka ɗauka suna maida numfarfashi, ahankali ya soma ɗanjin ƙarfi ajikinsa, kallon Zaleehan yayi, wanda ta riga da ta rufe jikinta da blanket, kyawawan idanunta alumshe suke, da'alama itama ta jigata sosai.

Towel ya jawo ya ɗaura ajikinsa, dayake wheelchair ɗinsa na gefen bed ɗin, shiyasa bai wani sha wahala ba wajen yunƙurin tashi, hawa kan wheelchair ɗin nasa yayi, cikin nutsuwa ya wuce bathroom,
da kansa ya haɗa musu ruwan wanka acikin wani haɗaɗɗen jakuzzie, saida ya tabbatar da ya shirya musu komai na wanka, kafun ya dawo cikin ɗakin, hannayensa yasa ya ɗagota jikinsa, ɗan shagwaɓe masa fuska tayi, tare da turo bakinta gaba, cikin sakalci tace.
"Dan Allah kabarni saida safe wallahi na gaji sosai, ni bazan iya wanka yanzu ba, jikina duk ciwo yake min."
Dogon hancinta ya ɗan ja, cikin body language ɗinsa yace.
"Ehem dole ki fadi haka ai, bayan kin gama moreni, har da ihunki."
Hararan wasa tayi masa tare da sake turo masa baki gaba.
Ɗaukanta yayi suka wuce bathroom.
Bayan sunyi wankan tsarki shida kansa yayi mata wanka, koda suka fito ma shiya tayata ta saka rigan bacci, sake kimtsa gadon nasu sukayi.
Tana rungume ajikinsa haka suka kwanta, da yake agajiye suke sosai basu wani jimaba

daddaɗan bacci ya ɗaukesu.

Ƙiran sallan asuban da yaji raɗau acikin kunnuwansa ne ya sashi ɗan ɓude idanunsa, baiyane yayi salati,    tare da ɗan janye jikinsa daga nata ya tashi zaune, miƙa yayi, tare da jawo wheelchair ɗinsa ya hau kai.
Toilet ya shiga ya ɗauro alwala,  yana fitowa ya saka wata farar jallabiya tare da ɗaura ƙatuwar rigar sanyi, ƙarasowa jinkin gadon yayi, ahankali ya shiga ɗan bubbuga ƙafan Zaleeha'n, cikin magagin bacci ta bude idanunta, ganin haka ya sashi juyawa ya nufi ƙofar fita daga  ɗakin.
Ganin fitansa yasa akasalance ta tashi ta wuce toilet.

Shikuwa Saifuddeen koda yabar cikin hotel ɗin,kai tsaye masallacin dake kusa da hotel ɗin ya nufa,  Sultan Ahmed Masjid, acan yayi sallan Asuba, tare da ɗaukan Alƙur'ani ya ɗan taɓa karatu, jin bacci acikin idanunsa ne ya sashi hawa kan kekensa, ya koma zuwa cikin hotel ɗin nasu.
Zaune ya samu Zaleeha akan sallaya tana karatun Alƙur'ani, gaba ɗaya zazzaƙan muryarta ya karaɗe ɗakin,  kallo ɗaya ya mata ya saki murmushi,   komawa kan gadon  yayi ya kwanta, dan bayaso ya katse ta daga karatun da take.      Ko mintuna 10 baiyi da kwanciya ba bacci ya ɗaukesa, Zaleeha kuwa koda ta kammala karatun idanu ta zuba masa, hakanan yanayinsu na jiya da dare ke dawo mata, idanunta taɗan lumshe, tare dason jiyo abun da taji kaman yana faɗa jiyan, tabbas idan kunnuwanta basu mata ƙarya ba,  jiya tajishi kaman yana wasu irin surutai, saidai kuma sanin cewa shiɗin baya magana yasa take ƙoƙarin ƙaryata kanta.

Hijabin dake jikinta ta cire sannan ta haye saman gadon ta kwanta, abayansa, tare dayin pillow da kafaɗansa.   Taɗan jima ahaka kafun bacci ɓarawo ya ɗauketa.

Ƙarfe 10 dai-dai suka farka atare, wanka suka sakeyi, koda suka fito waya ya ɗauka inda yayi musu oder'n takeaway.   Bajimawa kuwa aka kawo musu, saida sukaci abincin, kafun Zaleeha ta kimtsa kanta cikin wata haɗaɗɗiyar gown me taushi, da ɗan kwalin kayan ta yane kanta, sannan ta ɗaura wata jibgegiyar rigar sanyi akai, shiɗinma dai kayan sanyi ne ajikinsa.
Sunyi matuƙar yin kyau,  kasancewar ƙarfe 11:30 dai-dai zaiga Doctors din da zasu duba shi, hakan yasa suka fito hannunsu sarƙe acikin na juna.
A compound ɗin hotel ɗin, suka samu drivern da Dr.Acash ya turo musu, wanda shine zai kaisu asibitin.
Babu ɓata lokaci  kuwa suka shiga, driver'n yaja suka tafi.
Har ƙofar babban asibitin. *Acibadem Hastanesi Hospital Instanbull*    drivern ya sauƙesu, already sun  samu waƴanda zasu musu jagora zuwa cikin asibitin na jiransu,     hakanne ma yasa basu wani sha wahala ba suka samu ganawa da manya  manyan Doctors,  awani ɗan falo Zaleeha ta zauna, inda shi kuwa aka wuce dashi wani ɗaki na musamman, Dr.Acash Prasat da kuma sauran doctors ɗin suka kaishi, inda suka duƙufa akansa, suna duba larurar tasa.

  Sama da 40 minute suka ɗauka suna checking ɗinsa, wanda ahakane suka hango babban nasaran dake tattare dashi, dan kuwa daga yanzu zuwa ko yaushe zai iya miƙewa ya tsaya akan ƙafafunsa har ma ya taka, kaman yanda duk wani me lafiya ke takawa.

Cikin son ƙarfafa masa guiwa, tare da horas dashi, Dr. Acash ya miƙa masa hannu,  babu musu kuwa ya kama, ɗan ɗagosa Dr Acash ɗin yayi take kuwa sai gashi ya miƙe ya tsaya akan ƙafafunsa, saidai ƙafafun nasa naɗan rawa kaɗan-kaɗan,     tafi sauran Doctors ɗin sukayi, dan su kansu sunji daɗin hakan.   Ahankali yaɗan ɗaga ƙafansa na dama ya taka ta, ƙoƙarin ɗaga ɗayar ƙafartasa yayi itama ya takata, wani irin fitinenne daɗi ne ya rufeshi, a haka sukayi taku bakwai zuwa tara ya sake ɗaga kafar zai taku na goma, saidai jin tayi masa nauyi yasashi komawa ya zauna.
Tafi sukayi mishi sosai kana suka bashi shawarwarin.
Magunguna suka rubuta masa, tare da basa ƙarfin guiwan cewa yasa aransa cewa ko da yaushe zai iya taka ƙafafunsa yayi tafiya mai tsawo kamar da, sannan kuma yana ɗan gwada miƙewa tsaye yana tsayawa akan ƙafafunsa, da sannu ƙafafunsa zasu ware ya samu a rinƙa riƙeshi yana ɗan takawa.
Kana   sunce akwai alluran da za'a ke mishi duk bayan sati ɗaya, ana biyu kuma yazo nan asibitin a sashi a na'urarsu mai ɗan yiwa bayansu tausa, lissafin dai zai kaisu watanni uku rak, za'a gama mishi komai.
Godiya ya musu sosai,  kusan dai awa biyu suka share acikin asibitin  kafun ya fito suka tafi.

 Daga asibitin  Wani haɗaɗɗen gardeen Goztepe Garden Park instanbul.
Sukaje Wurine mai ɗan karen kyau da daɗin yanayi dasa shauƙi da nishaɗin ko ina an ƙawatashi da koraye da jajayen fulawi, ga wasu kujeru masu kyan gaske kana mutane kowa sabgar gabanshi yakeyi kowa ka gani da shigar kayan sanyi, kusan anan suka ƙare rabin wuninsu na ranan, dan sai dare sannan suka koma hotel ɗin bayan sunyi sallan isha a blue mosque sosai dai suka ɗan zazzagaya.

Suna shiga ɗaki kuwa Saifuddeen ya kamo Zaleehan zuwa jikinsa.

Wani irin hot kiss ya soma bata dan wani irin sha'awarta yakeji ko dan hakan bai rasa nasaba da fitinenne sanyin garin da kuma yanayin kaɗaicin da suke ciki su kaɗai gashi kuma itama so da tattali na musamman take bashi.       Laɓɓanta na ƙasa ya tsotsa ahankali ya sauƙe wani irin zazzafan numfashi,   ita kuwa Zaleeha hannayenta ta cusa acikin gashin kansa, cikin matsanancin shauƙinsa takai bakinta dai-dai saitin kunennsa, harshenta taɗan zaro tare da soma karkaɗawa acikin kunnensa, wani irin abu yaji tun daga kansa har ƙasan ƙafarsa, sake matseta yayi gam acikin jikinsa,   ahankali yasanya hannunsa tare da soma ƙoƙarin rabata da rigan jikinta, sam bata yi yunƙurin hanasa ba, dan ayanzu itama tana tsananin buƙatarsa, batasan me yasa ba, sam batajin fitinarsa na ginsan ta ko dan masifar sonsa da takeyine ya kuma haɗe da yanayin sanyin garin shiyasa sai takejin daɗin ɗumin jikinshi sai dai in an gama tayi luƙus tana tahaki da raki, ya lura Ameena ta fita dauriya da iya juriya ba raki,     cikin ƙanƙanin lokaci ya zare mata riga, hannayensa dake rawa ya ɗaura akan fararen breast dinta, wanda suke mugun ɗaukar hankalinsa, saboda sosai  breast ɗin nata ke da kyau,  ganinsu kaɗai ya na sa Saif ɗinsa magantuwa bare yanzu da ciki yasa su kayi tamtsan-tamtsan.
Hannunsa na hagu ya ɗaura akan bayanta, cikin salo yake mata tafiyar tsutsa.
Ɗago kanta tayi, inda ta zuba masa kyawawan idanunta, ahankali take ɓalle masa aninayen

gaban rigansa, har saida ta cire masa rigan, ahankali ta soma shafa chest ɗinsa, tare da ɗan zaro harshenta tana kaɗa masa shi in a sexy, ga kuma wani irin sexy look da take binsa dashi. Bazai iya jurewa hakan ba, cikin sauri ya kamo harshenta yana sotsa, yayinda breast ɗinta ke gogan chest ɗinsa. Da iya kiss kaɗai sun zautar da junansu, tuni suka maida kansu naked. Kasancewar azaune yake akan wata haɗaɗɗiyar kujera ita kuma tana zaune ne akan cinyarsa, hannayensa duka biyu yasanya inda ya kama ƙugunta, cikin wani irin salo ya ajiyeta akan Saif ɗinsa wanda tuntuni take neman inda zata shiga, ƙaƙƙarfan ajiyar zuciya suka sake atare, haɗi da nishi me ɗauke da zafi zafi, saida numfashinsu ya kusan ɗaukewa alokacin da Saif ɗinsa ya gama ratsa cikin jikinta, ahankali take ɗan jujjuya jikinta, wanda hakan yasa shi ƙara fita hayyacinsa, dan samun kansa yayi acikin wata international world.

Da ƙarfi yace.
"Uhhhhhh wash Allah na, ohoooo My shugar Baby".
da ƙarfi Zaleeha tayi mishi wani irin ramumar da ta sashi sakin wani mgnan.
"Ohhhh waiyo Baby".
Ido ta zubawa labbansa duk da ita kanta a gigice take tabbas ta jishi raɗau cikin kunnuwanta.
Haka yasa ta kara himmar ƙwazonta da kuzarinta, a fili yake cewa.
"Ohh yess Baby, thanks. I love you so much".
haka yayi ta surutai har saida samu gamsuwa kafin ya nutsu,
ita kuwa ƙin sauƙa tayi kan cinya sa cikin zuba mishi ido tace.
"Me kace? Mai maita min inji?".
Kanshi ya manna a ƙirjinta wai ya nuna mata bai gane me take cewa ba,
cikin sauri ta ɗago kanshi tare da cewa.
"Please kayi mgna mana kamar yadda kayi yanzu, da munayin..".
hannunshin ya ɗaga tare da juya mata alamun wai baya jinta kuma bai gane me take faɗin ba,
cikin mmki tace.
"Ya zaka cemin baka jina baka mgna bayan yanzu ka gama ihu da surutu Please tell me true,
ba yanzu kai mgna ba?".
Bakinshi ya taɓe tare da janyeta daga kan cinyarshi rubutu ya mata a wayarshi.
"Ke ban gane me kike nufiba kinji daɗinki kin gigice kinzo kina min wani zancen bayan kin gama moreni da iface-ifacenki".
Da sauri ta rubuta mishi.
"Ka gane kam ba yanzu ka gama yin mgnaba".
Da sauri ya rubuta mata.
"A a kam ke dai kin gigice kinata ihun tara min jama'u yanzu zakice nayi mgna, kai lallai Saif dina ya iya gigitarwa, tunda zaisa kiji kurma na magana".
Miƙa mata wayar yayi kana ya hau kekenshi ya nufi bathroom.

Yana shiga dariya yayi tayi tare da cewa.
"Meyasa nake kasa yin control ɗin kaina ne muddin ina tare da ita, gashi yanzu ta fara ganoni".
Miƙewa yayi daga kan kekenshi ya tsaya cis da sawunshi Allah da ikonshi yanzu ƙafafuwan basa rawa,
taku ya farayi a hankali sai gashi yana tafiya saɗab-saɗab a hankali,

godiya yayiwa Allah ganin yayi taku har biyar shi ɗaya jin ya gajine yasa ya zauna ya fara wonkan.

Ita kuwa Zaleeha wayarshi dake hannunta ne ya fara rigging ganin,
Sunan Adda Rahma ne yasata ɗagawa.
Bayan sun gaisane cikin sanyi tace.
"Adda Rahma kin san wani abu kuwa?".
Da sauri tace.
"A a sai kin faɗa".
Cikin sanyi tace.
"Adda Rahma anya kuwa Hamma Saif baya mgna?".
Cikin wani irin dariya Adda Rahma tace.
"Allah ko Zaleeha?".
Kai ta gyaɗa tare da cewa.
"Kai gsky Adda Rahma akwai lokutan da nakeji Hamma Saif yana mgna".
Cikin dakiya da danne dariyarta tace.
"Kamar wani lokacin kenan? Zaleeha".
Kai ta jinjina dan bazata iya fadar lokacin da yake mgnarba.
cikin sanyi tace.
"Ba damuwa sai na tabbatar zan gaya miki".
Cikin dariya tace.
"To Allah ya tabbatar mana. Yana ina yanzun".
"Amin Amin". Tace kana taci gaba da cewa.
"Ya shiga wonka".
da haka sukayi sallama.
Adda Rahma kuwa me take banda dariya cikin kula Ya Adnan yace.
"Lfy kuwa kiketa dariya".
Kai ta manna da jikinshi tare da cewa.
"Saifuddeen da Zaleeha ne suke bani dariya, waishi dole zai ɓoye mata yana mgna na kuma gano in yana sabis yana mgnar da baya sanin yanayi ita kuma bazata iya gaya mana ga lokacin da yake mgnar ba da kuma abinda yake faɗa".
Dariya sukayi baki ɗayansu kana ya Adnan yace.
"Zadai muga ƙarshen Game dinnan".

A can Instanbul kuwa tana katse kiran Adda Rahman.
Ta kira Aunty Lubna da wayarta,
bayan sun gaisa ne take tace.
"Uhum Aunty Lubna dan Allah inada tambaya?".
A hankali tace.
"Allah yasa na sani".
Dan tana cikin baccine kiran Zaleeha ya tashita daga baccin.
Ita kuwa Zaleeha kai ta ɗan dafe tare da cewa.
"Ni kam Aunty Lubna ko kuramema suna mgna ne in sunayin sex".

Cikin mmkin tambayar tace.
"A a wlh ban saniba, meya faru?".
gajeren tsaki taja kana tace.
"Shike nan tunda baki saniba saida safe".
Tana faɗin hakan ta katse kiran.
Ta miƙe ta nufi cikin ɗakin.
A bakin gado ta sameshi a zaune.
Bata kulashiba ta shiga tai wonka.
tana fitowa ta kimtsa kana a hankali tazo ta konta gefenshi,
tana son tayi nazari kan yadda zata fahimci abin da take zargin.

Juyowa yayi ya fuskanceta.
ita kuwa ganin haka ta konta rigingine janye rigarta tayi sama,
ɗan cikinta daya dunƙule ya koma gefe ta nuna mishi tare da cewa.
"Ya koma gefe tun ɗazu".
Kanshi ya jinjina tare da mata mgna in boddy language.
"To bari Abbanshi ya gyara mishi konciya".
Kai ta gyaɗa mishi tare da lumshe ido.

Shi kuwa tafin hannunshi yasa, kan cikin a hankali a hankali yake shafa cikin yana ɗan hura iskan bakinshi a kai,
a hankali taji yaron ya motsa, yayi ƙasa dan da gefe ya ɗan yi
Cikin sauri ta buɗe ido tare da cewa.
"Laah Hamma Saif kaji ya motsa ko?".
Kanshi ya jinjina mata tare da yiwa cikin nata kiss,
kana ya konta tare da jawo musu blanket.

*****

Bayan kwana biyar duk yadda Zaleeha taso ta gano gskyar abinda taji Hamma Saif yakiya dan sosai yawa bakinshi linzamin".

Yau tunda safe suka fita zaga gari dan zaman gidan ya ishesu sabida tun randa sukaje ganin likita basu sake fitaba iya karsu cikin hotel ɗin.

Jin Zaleeha nata cewa tana jin yunwa ne yasa kai tsaye suka wuce.
_South Africa restaurant in instanbull_ wurin mai ɗan karen kyau da ƙawa dagin itatuwa masu kyau da korayen bishiyoyi ƴan ƙogai-ƙogoi garuwa dake gudana a gefe,
wani irin sanyi wurin yake dashi,
Shawarma and pizza sukaci, sai zazzafan tea maiyin mgnanin sanyi da suka sha,
daga nan suka ɗan fara zazzagayawa wuraren wani wurin su hau abin hawa wani wurin suje da ƙafa ranar ma dai har, dare suka dawo.

So a gije suke shiyasa basu kula junaba haka suka kwana, washe gari da safe kuma Zaleeha tace yayi hakuri bacci takeji dole ya hakura.

A nan gida Nigeria kuma Yauwa Adda Rahma tazo,
dan zasuje gidan Ahmad ita da Raliya da Ameena zasu ƙara kikkimtsa musu gidan dan Ahmad yace.
Saifuddeen na dawowa su kuma zasu ƙaura.

Bayan sunyi komaine suka dawo nan Adda Rahman ke basu Ibrin yadda tayi da Zaleeha ai kuwa sunsha dariyar diramar tasu.

Allah ma yayi Hayatuddeen baya nan.
Yana can gidan Baba Bello dan Saifuddeen ya aikeshi ya kaiwa Baba bellon kuɗin cefane.

A tsakar gidan suke zaune su dukansu harda Matar Baba Bellon suna hirarsu da dariya.
Hayatuddeen ne ya ɗago kanshi da sauri jin wata zazzaƙar murya ta ratsosu,
cikin sauƙe ajiyan zuciya yace.
"Wow masha Allah".
Sai ya kuma kalli Baba Bellon da matarsa da suke haɗa baki wurin cewa.
"A a Zahra, sannu da zuwa".
Cikin nitsuwarta da sakin fuskarta tace.
"Yauwa kawu Bello".
Gefenshi Baba Bellon ya nuna mata tare da cewa.
"Taho nan ki zauna mamana".
Murmushi tayi kana ta cire takalmanta sannan ta hau kan taburmar gefenshi ta zauna tare da cewa.
"Kawu ina wuni".
"Lfy lau Alhamdulillah ya ƴar uwarta".
Cewar baba Bellon.
gyara mayafinta tayi ganin kallon da Hayatuddeen keyi mata,
shi kuwa Hayatuddeen ido ya tsareta dasu ƴarinya kekkewar matashi da bazata wuce 15 to 16 years ba, yar dumurmur da ita kekkyawa ajin forko fara ƙal-ƙal mai tarin nitsuwa.
Hararanshi tayi a fakaice ganin kallon da yake mata cikin kauda kai tace.
"Tana lfy kawu, itace ma ta tasoni yamma-yamma wai kwana biyu lfy baka kai mata ziyara ba".
murmushi yayi kana yace.
"Lfy lau Alhamdulillah dama niyata gobe zanje".
Kai ta gyaɗa kana ta kalli Iyya tare da cewa.
"Iya ina wuni".
"Lfy lau Mamanmu, ya Mamanki".
iya ta amsa mata tare da cewa.
"Ya karatu?".
Baki ta ɗan murguɗawa Hayatuddeen kana tace.

"Tana lfy ta gaidaki karatu Alhamdulillah".

Baba Bellon kuwa a hankali ya kalli Hayatuddeen tare da cewa.
"Auta kaga Zahra ɗiyar ƙanwata Rahima maisunan mamanmune ita shiyasa muke sonta sosai".
Wani sassanyan murmushi Hayatuddeen yayi karon forko da yaji ya juya ldanunshi kamar yadda Hamma Saif ɗinshi keyi cikin sanyi ya kalleta murmushi ya ɗanyi tare da kallonta ido cikin ido a hankali yace.
"I love You". Da sauri tayi ƙasa da kanta,
Baba Bellon kuwa da Iya ba gane abinda yace sukayi ba.
Ita kuwa shiru tayi tana kallon yatsun kafarshi,
jin yace mata.
"Tunda ni bazaki gaisheni ba bari ni in gaisheki, My dear wife ina wuni".
Murya can ƙasa tace.
"Lfy lau".
Murmushi yayi ganin tanata gyara maya finta can kuma sai ta ɗago kanta jin Autan Ummi na cewa.
"Baba Bellon zaku bani ita ko? Ku aura min ita, in na gama karatuna kafin nan itama ta kara girma ta dena murguɗawa mutane baki".
Dariya sosai Baba Bellon yayi kana yace.
"Munma baka autan Ummi".
Dariya iya tayi kana tace.
"lallai kam yau kazo a Sa'a kenan sarkin surutu".
Hannunshin yasa ya jawo wayar gabanta ya kuwa yi Sa'a babu password ,
number shi ya saka kana ya kira number ta fita.
shida kanshi ya samata sunan akan wayarta.
ita kuwa a hankali ta mike cikin sanyi tace.
"Baba Bellon bari to in tafi kar dare yayi dama Mamy tace kar in daɗe".
Miƙewa yayi tare da cewa.
"To muje in rakaki".
Dan haka suka saba in tazo shike rakata da sauri, shima Hayatuddeen ya miƙe tare suka sallami Iya kana suka fito,
Suna fitowa yace Baba Bellon.
"Baba tozo in maida ita tunda nima yanzu zan tafi".
Cikin halin girma Baba Bellon yace.
"A a jeka, gidan ba nisa nan layin gwamnan Yobe ne da ƙafa zan rakata,
tura baki Hayatuddeen yayi kana yace.
"To kazo mu maida ita sai in dawo da kai".
To hakan fa akayi Baba Bellon na gaba a gefenshi bisa kujerar mai zaman banza ita kuwa tana baya ya tsaida madubin shi kan fuskarta.
A haka suka isa ƙofar gidansu mai kyau dai-dai misali bayan ta shigane shi kuma ya juya ya maida Baba Bellon kafin ya koma gida.

Yana isa kuwa ya zauna gaban Ummi da Adda Rahma cikin zumuɗin shi yace.

"Ummi na girma ko?".
Dariya tayi tare da cewa.
"Sosai ma kuwa".
Kanshi ya gyaɗa kana ya miƙe ya nufin ɗakinshi.

Su kuwa su Ummi mamaki sukeyi meyasa yayi wannan tambayar.

Shi kuwa Hayatuddeen kan gadon shi ya hau tare da cewa.
"Aha tunda na girma ai sai in fara neman aure, bazan gaya kowa naga matar da nake so ba sai Hamma na kadai in ya yarde min dai bani da matsala.
Ganin magriba tayine ya miƙe ya shiga bathroom dan yin al'wala.

***

Yau kwanansu Hamma Saif goma cib a instanbul kuma yau kwana uku kenan bai samu damar lallatse Zaleeha ba,
ita kuwa Zaleeha bata cika son takurar bane, dan sosai cikinta ke mata nauyi like cikin wata Bakwai sam bazakace cikin wata huɗu ana biyar bane,
yanzu kullum kamar kara mishi girma akeyi dan ya fito sosai hips ɗinta kuwa sai hauhawa sukeyi.

Yau tunda safe take ta binshi su fita suga gari yaƙi sauraron ta a ƙarshe ma cewa yayi sai in zata bashi abibln daɗinshi, to tana son yawon shiyasa cikin jin daɗi tace.
"Eh na yarda amman sai dare in mun dawo".
Kanshi ya gyaɗa kana yaci gaba da chatting ɗin da yakeyi da Ameena.

Har saida sukayi sallan magriba da isha kana suka fita.

The best shapping street in Instabull suka bi,
inda titin yake tamkar kasuwa babu abinda babu a sashin wurin kowa ka gani hidimar gabanshi yakeyi,
darene amman kamar rana,
Da yake tattaki sukeyi da ƙafa dan bazasuyi nisa sosaiba tunda sai dare suka fito,
Wani kekyawan Restaurant suka shiga Sovor Restaurant wurine mai masifar kyau da ɗaukan hankali da ban sha'awa an zagaye wurin da glass mai ruwan garai-garai ga korayen shuke-shuke daga ƙasa kuma ruwane ke gudana,
Turawane a cike a wurin sai tsirarun baƙaƙen fata,
kowa sabgar gabanshi keyi,
suna cikin cin abinci wani irin sanyi ya fara ratsasu, gaba ɗaya kowa sai gyara rigar jikinsa keyi, sabida sanyi dake ratsotsu,
murmushi Saifuddeen yayi ganin yadda Zaleeha keta karkarwa, hakan ne yasa yace a kawo mata zazzafan tea,
koda aka kawo kofuna biyu nashi da nata,

hararan kofunan tayi tare da cewa.
"Hegu marowata sai suke bawa mutane abu ɗan kaɗan su karɓi kuɗi da yawa".
Ta ƙarishe mgnar tana zuƙe shayin,
ganin haka ya miƙa mata ɗaya kofin shima zuƙeshi tayi tas kana tace.
"Ai kuwa na ɗanjj ɗumi a hanjina, haba gari sai kace masifa sanyi ba sauƙi".
Ido ta zubawa inda yake nuna mata da hannunshin da sauri tace.
"Kai Hamma Saif ruwan dusan ƙanƙara akeyi, mu tafi gida".
Kai ya gyaɗa mata dan gaba ɗaya rabin mutanen wurin duk sun mimmiƙe alamun zasu tattafi mafakarsu.
Bayan ya biya kuɗin ne, kana ya saya mata ɗan abinda zataci da dare sannan suka fito suka nufi gida.
Hannunta na cikin nashi kar-kar taketa rawan sanyi sabida sosai dusar ƙanƙara ke zubowa a kansu,
cikin rawan sanyi tace.
"Hahhh Hamma Saif mugudu, kai baka jin sanyin ne.
Kallifa duk dusar ƙanƙara a kanka".
hannunta ɗaya tasa tana ɗan kaɗe mishi.
A haka dai suka iso masauƙinsu da yake ba nisa sosai.

Suna shiga falon ya sake hannunta gaban dandamalin nan na hura wuta ya tsaya,
wutar ya hura kamar yadda yaga suna hurawa.
Da sauri ta karaso kan cinyarshi ta zauna ta manna bayanta da ƙirjinshi,
shi kuwa Saifuddeen tafin hannunshi yasa kusa da wutan saida yaji sunyi zafi jau-jau kana a hankali ya ɗage rigarta cikinta ya baiyana, hannunshin ya daura kan cikin nata,
Ido ta lumshe jin ɗunmin hannunshi ya ratsata mata fatar cikinta har abinda ke cikin ya motsa a hankali,
shi kuwa Hamma Saif sake maida hannun yayi jikin wutan saida sukayi zafi sosai kana,
ya mannasu kan cikinta yana shafa cikin yana ɗunɗumashi murmushi tayi gane nufunshi wato ɗanshi yake jiyawa tsoro sanyin shine harda ɗunɗuma mata cikin, a hankali tace.
"Nima ai Baba Malam ɗinmu na sona, da yasan a sanyin nan zaka kawoni kaita luguiguitani da yace a barni a gida."
Murmushi yayi jin kalamanta.
A rashin yace
"Ni kuma ai kece ɗumina".
haka yayita ɗunɗumata kab jikinta kana ya rage wutan sannan ya wuce bedroom da ita a bisa cinyarshin.

Suna shiga ya ajiyeta kan gado,
kana shima ya hau, cikin borgon suka shiga,
jawota jikinshi yayi bayan ya cire mata kayan jikinta.
Cikin kiɗima da begenshi ta ruggumeshi dan Allah ya sani tayi kewa shi,
bakinsu ta haɗe suna sumbatar juna,
hannunshin yasa yanata shafa dukkan jikinta,

a take suka fara dimaucewa,
da sauri ta ɗan yunƙura ta tashi zaune dan so take ta sarrafashi da kanta.
kan cinyarshi ta zauna, tare da kamo hannunshi ɗaya ta ɗaura kan ƙirjinta na hagu,
A hankali tasa hannuntan na dama ta tallabo breast ɗinta na dama,
kana tasa hannu ta jawo kanshi kamar yadda uwa ke likawa ɗanta breast a baki haka ta bashi
ai kuwa a buƙace ya cabke da karfi tace.
"Wash darling so sweet".
a hankali suka gigice,
duk da ita Zaleeha tana ta son ta iya sarrafa nitsuwarta dan gaskata wani abun.
shiyasa taji zazzafan nishin da Hamma Saif ɗin yayi lokacin data haɗe jikinsu ras ta ji muryarshi
daya kasa dannewa yana cewa.
"Yess! Hshhhhhhh yesss!! Yessss!!! ohh yess!!!! Suger baby, yahhhhhh I love you I love you I
love you so much, thanks my dear".
Murmushi tayi tare da cewa.
"Faɗa da ƙarfi kana jin daɗi."
Cikin gigita ya rinka gyada mata kanshi tare da cewa.
"Wayyo Allah sosai ma yi da sauri-sauri da ƙarfi-karfi shugar Baby".
cikin rawan murya tace.
"Kurma mai maganan dare".
Ihu yasa jin yadda ta nitsashi da ƙarfi yace.
"Ihun dole ne in ana sex da zazzafar mace irinki".
Murmushi tayi kana ta koma ta konta,
ai kuwa da zafinshi ya bita,
haka ya rinƙa surutai da ihu,
har saida ya samu gamsuwa.

Bayan sunyi wonkane suka dawo suka konta,
bata kulashiba sukayi bacci.

Saida safe bayan sunje Oasis Restaurant dake nan cikin hotel din nasune sunci sun sha sunyi
haniƙan,
kafin sukaje asibiti aka dubashi.
Bayan sun dawone sai suka konta dan yin bacci dan daren jiya basuyi bacci sosai ba.
Cikin sanyi ta kalleshi tare da cewa.
"Me ma kayi ta cewa jiya da dare?".
Shareta yayi kamar bai jitaba bare ya gane abinda tace,
ganin haka yasa bata kulashiba,
wayarta ta jawo Ummi ta kira bayan sun gaisa tace.
"Ummi ba kwanaki nace miki ina zaton Hamma Saif yana mgna ba?".
Cikin murmushi Ummi tace.
"Eh haka dai akayi".
Da sauri tace.
"To wlh Ummi Hamma Saif yana mgna".

Da sauri Ummi tace.
"Kai Zaleeha yana magana to ina yake bani shi muyi mgna inji muryar Babana".
Cikin sanyi tace.
"To ai Ummi ba ko yaushe yake mgna ba".
Da mmki Ummi da bata gane madosar mgnarba tace.
"To sai yaushe yakeyin mgna?".
Cikin sanyi tace.
"Sai tsakiyar dare fa nakejin shi yana mgnar".
Jin haka yasa Ummi tayi saurin kashe wayar
ita kuwa Zaleeha dama da gaiya tayi wai ko zai gaya mata gsky,
ganin bai kulata bane ta kuma kiran ya Ahmad cikin sanyi tace.
"Wlh ko Ya Ahmad Hamma Saif yana mgna".
Cikin dariya Ahmad yace.
"Kai Zaleeha kawai dai yanzu kina sonshine shiyasa har kikji da ganin kamar yana mgna sabida soyayya tayi daɗi".
Da sauri tace.
"Allah ko Ya  Ahmad wlh tallahi yana mgna".
Dariya yayi tare da cewa.
"To bani shi mu gaisa".
Cikin tura baki tace.
"To ai ba yanzu yake mgnarba fa Ya Ahmad". cikin dariya yace.
"Ikon Allah to sai yaushe yake magana?".
A hankali tace.
"Sai tsakiyar dare yaketa mgna".
Da sauri ta katse kiran jin wani irin dariyan da Ya Ahmad ɗin nata ya fashe dashi.
cikin hararanshi tace to wlh.
"Sai na tambayi Ummu Adeel ai ita kam matarkace zata sani kuma ba kunya zan gaya mata lokacin da kake mgn".
Tana gama fadin haka ta juya mishi baya tare da kiran Ameena.
Shi kuwa Saifuddeen dariya yake tayi can ƙasa ƙasa sabida yadda take cewa mutane wai sai tsakar dare yake mgna, da zaran an tambaye me yake cewa sai ta kashe wayar.

Ameena kuwa tana zaune a falonta taga kiran Zaleeha tana ɗagawa tace.
"Muna kewarki Ammin Adeel".
Murmushi Zaleeha tayi kana tace.
"Nima ina kewarku ina ɗan al'barka?".

"Gashi nan yanata baccinsa bayan ya gama kiranki ke da Abbanshi".

Murmushi tayi kana tace.
"A shafa min kanshi".
Hannu tasa ta shafa kan Adeel tare da cewa.
"Na shafa kanshi".

Murmushi Zaleeha tayi kana a hankali tace.
"Yauwa dan Allah Ummu Adeel, in tambayeki wani abu mana in ranki bazai ɓaci ba?".

A hankali Ameena tace.
"Ba komai Allah yasa na sani".
Amin Amin tace kana ta ɗanyi ƙasa da murya tare da cewa.
"Dan Allah Ummu Adeel kin san Hamma Saif yana mgna a wasu lokutan?".
Cikin nuna bata saniba dan bin umarnin mijinta tunda shi yace karta gayawa Zaleeha yanaji da mgna a hankali tace.
"Mgna kuma kai a a kam yaushe ya fara mgnar a wasu lokutan yake mgnar?".
Fuska ta ɗan yamutsa tare da cewa.
"Ummu Adeel tsakaninki da Allah in Hamma Saif yanayin sex baya mgna?".
Wani katon dutsen baƙin cikin kishine ya danni maƙoshin Ameena da kyar ta iya fisgo dariya mai ƙarfi.
Jin hakane kawai Zaleeha tace.
"Shike nan kowa sai yata dariya keda ya kamata ki gaya min ma kinƙi".
Tana kaiwa nan ta kashe,
zuwa yanzu ta fara zargin ko sai in yana sex da itane kawai yake iya iya mgna wata ƙil shima baisan yana mgnarba, wannan tunaninne yasa ta turawae Rashida text kamar haka.
"Slm My friend dan Allah ga tambayata ki tambayarmin Malam Ishaq amman karkice masa nice, ki tambayan minshi wai kurma na iya mgna ne in yana taraiya da iyali shi".
Tana tura saƙon ta koma ta konta tanata saƙe-saƙe a ranta a hakan sukayi bacci.

Washe gari da yamma suna konce kan gadon kamar jiya, taita tambayarsu kam taji yana mgna ya nuna mata dadɗine yasata takejin kamar yana mgna Saif ɗinshi ke kai mata karo.

Hakan yasa ta kira Aunty Lubna.
Tana ɗagawa suka gaisa kana a hankali tace.
"Wlh Aunty Lubna kaina na ɗaurewa sosai kan Hamma Saif, wlh yana mgna".
Da sauri Aunty Lubna tace.
"To wai me yake cewa".
Cikin sanyi tace.
"Bari in gaya miki sanda yake mgna da abinda yake cewa".
Da sauri Saifuddeen ya buɗe idonshi dan jin wai zata gayawa Aunty Lubna abinda yake cewa da kuma lokacin da yake mgna.
Ita kuwa Aunty Lubna a hankali tace.
"Ina jinki".
Cikin sauƙe numfashin da ɗan naga sauti bayan ta katse kiran amman sai tayi kamar kiran nasu na haɗe murya ta ɗan ƙara ɗagawa tace.
"Aunty Lubna wlh da dare yake mgna kuma cewa yake.
"Waiyy shugar baby yess....".
Da sauri cikin karfi Saifuddeen ya cilla wayar gefe tare dasa tafin hannunshi ya rufe mata

bakinta, cikin mamaki yace.
"Na tuba karki gayawa mutane abinda nake cewa. Ina magana kinjiko ina ji kuma ina magana, na tuba ki rufa mana asirinmu karki gaya mata abinda nake cewa da wani idon zan kallesu, ina mgna, kawai dan kiyi ta surutu ina jinki ina dariya yasa na ɓoye miki.
Na tuba my happiness my everything My shugar mai zumar rayuwata, i love You 1 i love You 2 3,4,5,6,7,8,9,10,11, i love You dozin-dozin Zaleehan Hamma Saif".
Wata iriyar rugguma tayi mishi tare da cewa.
"I love You too my Notyart, Alhamdulillah ya Allah na gode maka".
Sai ta kuma rinƙa kissing nashi tako ina tana shunshunar ƙamshin jikinta ji take kamar ta maidashi cikin jikinta.
Murmushi yayi tayi tare da cewa.
"Kurma mai mgna dare ko? Ba haka kika ce minba ranar, kema kuma ihun daɗi kiketayi".
Sai ta kuma sakeshi tare da juya mishi baya cikin sanyi tace.
"Nayi fushi da kai meyasa zaka ɓoye min bayan kasan ina sonka ina son samun Ifyarka".
Kunnenshi ya riƙe tare da cewa.
"Na tuba ki yafe min".
Kafaɗa ta maƙe,
juyota yayi suna fuskantar juna kana a hankali yace.
"To taso kiji wani abun daɗi so sweet ba haka kike cewa ba".
Ido ta lumshe kana ta tashi zaune,
cikin sanyi tace.
"Gaya min menene abin daɗin?".
Motsota yayi yasa tafin hannunshi yana shafa cikin nasu cikin wani yanayin zazzafan so yace.
"Duk kowa yasan inaji ina mgna shiyasa suketa miki dariya, sabida su-sun-san tun randa na karɓi budrcinki da kika rinƙa zunɗuma min ihu da kururuwa a kunnena tun ranan kunnena ya buɗu kuma ina mgna.
My happiness muryarki na faraji bayan tsawon shekara ashirin banyi mgna ba banjiba, daga sunan Allah dana kira kuma sunanki ne na biyu dana kira".
Ruggumeshi tayi gam jikinta Dan tuno irin surutan da tayi tayi a zatonta baya jinta ashe shuka takeyi a idanun makorwa,
Ruggumeta yayi gam shima kana ya ɗan kamo fuskaceta cikin sanyi yace.
"Yauwa duk sun rigaki sanin na worke inaji ina mgna to ke kuma zaki rigasu sanin na worke ina tsayuwa da ƙafafuna kuma ina ƴar gajerar tafiya, bazan gaya musuba sai mun koma,".
Da sauri tace.
"Harda Ummi? Bazaka gaya mata kana tafiyaba wayyo daɗi wayyo Hamma Saif farin cikina bazai misaltuba Hamma Saif Allah yana sona yana sonmu, amman ni kam bazan iyaba zan gayawa Ummi".
Kai ya jujjuya mata baki ta a hankali yace.
"Ban yarda".
Cikin sanyi tace.
"Meyasa?".
Cikin sanyi yace.
"Sabida nafi son mu kara daɗewa ina worke garau kafin  mu koma, in shiga gidana da ƙafafuna,

inje gaban Ummina a tsaye da sawuna, ina son inga irin farin cikin da zatayi in taga ina tafiya.
Sannan kuwa inaso muyi zamanmu a nan muyi amarcinmu mu raini cikinmu mu mori ƙuruciyarmj kafin mu koma ya zama kwana bibbiyu kawai zanke ganinki, kuma kinga Ummu Adeel ma wata biyu da mako uku mukayi a India da ita dan haka kema wata uku zamuyi, kafin nan cikinmu yayi wata bakwai, muna komawa muyi wata biyu da sati biyu a 9Ja sai muce saudia gaba ɗayanmu ki haihu a can".
Tura baki tayi. Cikin sanyi tace.
"Ai da kana sona da bakayi min kishiyaba da ka jirani in gudu in dawo ɗin muyi zamanmu mu biyu, in ganka sanda nakeso, amman ina guduwa ka danƙaromin kishi, kuma ko kuɗin faɗar kishiya ni ba'a banba babu wanda ya danne min ƙirji wato in na ga dama ƙirjin ya fashe".
Lakace kumatunta yayi tare da cewa.
"To ni dai ba laifina bane Baba Malam nefa yamin auren gata tunda yaga ke kin gudu bakya son inji daɗi dake, keda bakya sona me ruwanki da kishina".
Ture hannunshi tayi tuni hawaye sun cika mata ido.
Haka nan yau taji kishi, kumallon mata fahimtar hakanne ya sashi ruggumeta suka faɗa duniyar ma'aurata yanayi yana raɗa mata zafafan kalaman da dole taji sanyi a ranta.
"My first love, kada kiyi fushi da Malam Caifuddeen ɗinki, ina sonki son da ban san adadinshi ba, ke ta musamman ce a rayuwata,
Ai ƙarin aure ba laifi bane, bakya son inji daɗi kan daɗi ne".
A hankali tace.
"Ina so mana, shiyasa nake son duk wani abu naka da kakeson".
Shafa kanta yayi lokacin daya haɗesu wuri ɗaya a hankali yace.
"Na sani, nasan kina son duk wani abu da nakeso, kin son Adeel ɗina tamkar ke kika haife min shi, kin danne kishinki kin zauna da mamanshi Ify".
Ruggumeshi tayi tare cewa.
"Adeel ai ɗa nane gajin haƙurinka da zalamarka ne yasa ka ɗirkawa babarshi cikinshi, bakaga dani yake Mamaba".
Lakace hancinta yayi tare da cewa.
"To ai kema gashi na ɗirka miki naki, ba cuta ba cutarwa ko, Baby mai Rafin daɗi".
Daga magna ta gagaresu sukaci gaba da shawagi a duniyar masoya.
Koda suka dawo haiyacinsu miƙewa zaune yayi kana cikin sanyi yace.
"Taso kizo ki tsaya a gabana.
Doctors sunce a rinƙa min tete tafiyata zata miƙa da wuri".
Da sauri ta sauƙo towel ta ɗaura kana ta miƙo mishi hannunta ya riƙe sannan ya tashi tsaye a hankali ta fara yin baya yana binta a murmushi yake tayi ganin cikinsu a tsakiyarsu,
Allah cikin ikonsa sai gashi sun isa har cikin bathroom suna,
shiga sukayi wonka a tare,
har zasu fito tare tace.
"Yauwa my love jirani bari inzo karfa ka fito".
Murmushi yayi kana yace.
"Ok to kiyi sauri".
"To". tace kana ta fita tana shiga ɗakin doguwar rigarta ta zura sannan ta ɗauki wayarshi.
Ummi ta kira video call sai ta haɗa kiran da System ɗinshi, ta saita fuskar laptop ɗin da hanyar

fitowa bathroom ɗin nasu,
dai-dai lokacin kuma Ummi ta amsa kiran ganin fuskar Zaleeha yasa tayi dariya tare da cewa.
"Ƴar al'barka yanzu nake mgnanku da Ummansu Ishaq".
Da sauri Zaleeha tayi ƙasa da Murya tare da cewa Ummi.
"Ummi kiyi shiru bari kiga wani abu".
Da sauri tace.
"To". Sai kuma taga Zaleeha ta nufi cikin bathroom ɗin hannunta na riƙe da tattausar baƙar jallabiya.

Tana shiga ta miƙa mishi tace.
"Yau saka My shugar Hammana mai abin daɗin sa ihu, sai ka gwada fita da ƙafafuwan mu gani, dan nafi son inga kana tafiya kai ɗaya".
Cikin ƙarfin hali yace.
"To mai rafin daɗin za'ayi yadda kikeso ko dan kiyi ta barina  ina shiga rafinmu nan mai daɗin".
Ya ƙarashe mgnar yana zira rigar.

har ƙasa ta sauƙo cikin jin daɗi tace.
"To Ya Habibi kayi gaba ina binka a baya".
Kai ya gyaɗa mata kana a hankali ya fara taku,
suna isa baƙin ƙofar tayi maza ta buɗe mishi ƙofar da ƙar damanshi ya fara  ɗagawa da niyar yin takun fitowan,
 ita kuwa tana biye dashi a baya.

Cikin mmki Ummi ta zubawa wayarta ido,
ganin ta....!

*NAKASA BA KASAWA BACE*

NA
*AYSHA ALIYU GARKUWA*

Part 3.    Page 1-to-5

_LITTAFINA na KUƊINE ki biya ki karanta ba tare da haƙƙin kowa a kankiba, turo katin mtn na ɗari uku kacal ta wannan layin 09097853276 ko kuma kiyi min transfer ɗari ukun ta asusuna na 0005388578 jaiz back Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo min screenshort shaidar biyanki ta dai wannan number da nakeyi chatting da ita 09097853276_

Dan Allah ku dena tura min littafina Hukuncin Allah a groups ɗin NAKASA Ba KASAWA BACE, shima na kuɗine kuma wasu basu sayaba, bawai fans ɗin Hukuncin Allah kaɗai bane suka sayi

wannan littafin akwai sabbin da a ƙiyasci sunfi ɗari uku da hamsin.

In zaki sayi littafina ki tabbatar kinada App ɗin WPS office.

By
*GARKUWAR FULANI*

Da sauri Ummi ta zuwa wayar ido.
ɗut ɗut haka taji ƙiran ya yanke, da alama network ne ya katse ƙiran, fuska ɗauke da mamaki take kallon screen din wayar, aɗan bayyane tace.
"To meyasa ƙiran kuma ya katse, ko me Zaleeha ke son nunamin?". sake dialing numbern tayi amma taji baya shiga.

Zaleeha kuwa tafi take masa da hannunta, cikin matsanancin farinciki batare da sanin ƙiran da tayiwa Ummin ya katse ba tace.
"Wonderful Ummi kinga Hamma Saif ko, Ummi ya warke yafara takawa da ƙafafunsa."
Ta ƙare maganar tana me ɗaukan laptop ɗinsa, gani tayi gaba ɗaya ƙiran ya katse, tun tsawon mintuna 4 da suka wuce. Fuska taɗan kwaɓe tare da dafe kanta, cikin takaici tace.
"Wallahi Hamma Saif saika sanja laptop wannan laptop ɗin naka bata da kyau."
Tafaɗi maganan tana ɗan bubbuga laptop ɗin nasa.
Hannu yasa ya jawota tare da karɓe laptop ɗinsa, cikin yanayin mamaki yace.
"Dama me kike ƙoƙarin yi?".
Bakinta ta turo gaba, ashagwaɓe tace.
"Waifa connecting vedio call nayi, inason nunawa Ummi tafiyanka shine kuma ashe kiran ya ya katse tun kafin mu fito". Idanunsa ya ɗan zuba mata, ahankali yaja hannunta suka zauna akan gado, cikin kulawa yace.
"Nagodewa Allah ma da ƙiran ya katse, da shikenan yanzu kin ɓatamin plant, kingani ai Allah na ya kamaki." Kallonsa tayi alaman "Kamar ya?".
Kai ya jinjina tare da cewa.
"Yeah ba nacemiki banason Ummi tasan ina takawa, ba Ummi bama kowa banaso ya sani, nafison nayi surprising nasu, shiyasa nace karmu faɗa musu shine wato bakya jin mgnata kike son faɗa musu.
Nafison nayi surprising ɗin su zasufi jin farin ciki Ko bakyason haka?."
Ya ƙarishe maganar yana me ɗan shafa kanta.
Gane nufinsa yasa tayi murmushi tare da cewa. "Inaso mana, amma nasan su Ummi zasuji dadi sosai, Allah sarki Ummi nasan saitafi kowa jin daɗi".
Kallonta yayi cikin nutsuwa yace.
"Saitafi kowa kuma, kice dai saitafi kowa kuma ya fiki".
Ya ƙarishe mgnar cikin tsokana.
Ɗan hararan wasa ta jefa masa, ido cikin ido tace. "Hmmm saidai ita ɗin ne kaɗai zata fini amma ba kowa a duniya da zai fini jin daɗin samun lfyarka, kai bakasan cewa aduniya daga

Ummi asonka sai ni ba, bayan Ummi babu meyi maka irin son danake ma, saidai duk sauran mutane su biyo bayana." Dariya yayi, har saida dimples ɗinsa suka lotsa, cikin son tsokanarta yace.
"Ummm ashe ana sona kuma aka gudu, aka tafi can wata duniya".
Ɗan dukan wasa ta kai masa, cikin kulawa tace. "To nasan kaine? ai da nasan kaine bazan gudu ba, kuma ai duk kaine ka jawo, da ace tun alokacin ka nunamin real face dinka, ai bazan gudu ba, zan zauna atare dakai, kuma dama ai ni ba tsananka nayi ba, kawai dai dan inada wanda nake sone mara saje kai kuma na ganka da saje kuma ka ƙara dari da kyau da girma da kwarjini da ƴar ƙiba kuma kana bisa kujerar mulki ya zanyi in ganeka"
Murmushi ya ɗanyi tare da cewa.
"Duk a cikin shekara ɗayan nayi waɗannan abubuwan da kika lissafi?".
Sajenshi ta shafa tare da cewa.
"Eh mana, sai dai duk sanda naga idanunka sai inga kamar na sansu". Idanunsa yaɗan juya, cikin kulawa yace. "Hahhh to ina wanda kikeso ɗin?".
Da hannunta ta nunasa alaman gaka.
Yana murmushi yajawota jikinsa ya rungumeta, tabbas yanason Zaleeha so me tsanani, yanajin ƙaunarta sosai acikin ransa, yayi imani itace macen da ta dace da rayuwarsa, itace kuma dai-dai da tsarinsa, duk da kasancewar Ameena ta shigo cikin rayuwarsa, alokacin da baya buƙata, ta kuma zauna dashi da lalurarsa, hakan shiyasa ya bata wani babban gurbi a rayuwarsa.
Amma Zaleeha itace tauraruwarsa har gaban abada.

Hira suka ɗan taɓa kaɗan, jin ana ƙiran sallan magriba ne ya sashi ɗauro alwala ya wuce masallacin.
Sultan Ahmed Masjid dake kusa da masauƙin nasu, itama Zaleehan alwala tayi sannan ta zo ta gabatar da sallah, koda ta idar bata tashi akan sallayan ba, saida tayi sallan isha, yau kam batajin zuwa restaurant cin abinci, zatace Saifuddeen ɗin ya musu order kawai, dan sosai sanyi ya shiga jikinta ayƴan kwanakin nan shiasa ma batason sake fita.
Kayan jikinta ta cire, sannan ta saka wata ƴar ficikar rigar bacci, wanda da ita da babu duk ɗaya suke, tana kammala shafa fitinannen turarenta Saifuddeen ya turo ƙofar ɗakin ya shigo.
Murmushi suka sakarwa juna, hannunsa ya buɗe mata babu musu kuwa taje ta shige jikinsa, cikinta yaɗan shafa, tare da yi mata alaman "Yunwa ko?".
Kai ta gyaɗa masa alaman "Eh." Waya ya bugawa masu kawo abinci hotel ɗin, inda ya gaya musu favorite ɗin da za'a kawo musu.
Ko mintuna goma ba ayi ba kuwa saiga abincin nasu ya iso.
Ɗaurata yayi akan cinyarsa, shi da kansa ya ciyar da ita, saida ya tabbatar ta ƙoshi sannan shima yaci, koda suka kammala brush sukayi sannan suka kwanta rungume da juna, da yake agajiye suke shiyasa basuyi wani abu ba, saidai Saifuddeen da jarabarsa ta kasa barinsa, dole haka saida ya mammatse ta, har saida taji breast ɗinta na mata zogi, haka sukayi bacci, bakinsa na kan nipples ɗinta.

Washegari kuwa koda sukayi sallan asuba, bacci suka sake komawa, dan ita Zaleeha yanzu kwata-kwata bata gajiya da bacci.

Basu suka tashi ba kuwa sai ƙarfe 9.
Kaman jiya da dare haka yau ma aka kawo musu break fast, bayan sunci abincin ne, Zaleeha tasa masa daru kan cewar lallai sai dai yazo suyi wanka a swimming.
Biye mata yayi suka shiga swimming pool ɗin, wanka sukayi haɗi da zazzafan romance.
Sunjima acikin ruwan kafun suka fito, anan falo suka zauna inda tayi pillow da cinyansa. Wani latest film yasa musu a laptop ɗinsa suka kalla.
Suna cikin kallone bacci ya ɗauketa, akan gado ya shumfuɗeta, sannan ya ɗauki wayansa dake ta faman tsuwa, ganin sunan Ishaq na yawo akan screen ɗin wayar ya sashi amsa ƙiran da sauri.
Daga can Ishaq ya saki dariyan mugunta, cikin salon tsokana yace. "Kaga Kurma me maganan dare, wallahi kana sha'aninka, wato kasamu yar mutane kana mata sambatu ko". Dariya Saifudddeen ɗin yayi tare da ɗan shafa sumar kansa, yace "Wallahi Ishaq kai banza ne ni ba abinda nayi". Dariya Ishaq ɗin yayi, tare da cewa.
"Eh mana, dole ai kace haka, to duk dai bawannan ba ya ƙarfin jikin naka, nasan zuwa yanzu ansamu cigaba." Kai yajinjina kaman Ishaq ɗin nagabansa yace.
"Ansamu cigaba sosai ma."
Cikin jin daɗi Ishaq yace.
"Alhamdulillah abun da muke fata daso kenan, to ya Zaleeha fatan dai baka sake mata magana cikin dare ba".
Murmushi yayi tare dakai dubansa gareta, har yanzu baccinta take sha. "Meza afasa kaida kasani, saidai danaga tana ƙoƙarin min bankaɗa awajen Auntynta na faɗa mata cewar ina magana." Dariya sosai Ishaq yayi tare da cewa.
"Masha Allah ai hakan yayi."
Hira suka ɗan taɓa kaɗan da Ishaq ɗin sannan sukayi sallama, Ishaq na katse ƙiran ya tashi ya koma falo, numbern Ameena yayi dialing bugu biyu kuwa ta ɗauka.
Hira suka sha sosai da ita, sai faman faɗa masa yanda tayi missing ɗinsa take, haka dai ya biye mata saida suka kwashe minti 30 suna waya, sannan daga bisani sukayi sallama, jin zaman shiru ya ishesa ne, ya sashi ɗaukan Laptop ɗinsa ya fara gudanar da wani aiki.
Haka dai awannan rana babu inda sukaje, duk agida suka wuni.

Washegari kuwa tun da sukayi break Zaleeha ta matsa masa akan cewa tanaso taɗan sake zaga gari, da yake shima yana da buƙatar hakan shiyasa baiƙi ba, dan yanaso yaɗan tattaka ƙafafunsa, yasan da haka zai ware.
Kusan shiga iri ɗaya sukayi, koda suka fita sunyi kyau gwanin ban sha'awa, kasancewar ba wani tafiya me tsawo zasuyi ba,
shiyasa basu nemi mota ba, idan suka ɗanyi tafiya me ɗan tsawo, sai ya ce ta tsaya, shida kansa yake miƙewa akan kekensa, ahankali yake ɗan taka ƙafafunsa, cikin ikon Allah kuwa sai gashi yana ɗan iyayin tafiya me tsawo, idan yayi tafiya me nisa kuwa sai itace zata biyosa da wheelchair ɗinsa, Alhamdulillah dan bayajin ƙafar nayi masa zafi.

Bayan sati uku yawanci suna fita suyi tattakin.
Kuma Alhamdulillah yanzu tafiyarshi na ɗan nisa,
Yau da yamma suka fito,

koda motarsu ta kawosu tsakiyar garin sai sukace ya koma sai sun nemishi yazo ɗauka su.
anan kan Babban titin Instanbul ɗin suketa tattaki,
suna tafiya ya ɗan kalleta a hankali yace.
"Bari in tashi in tafi har can, kinga can wurin da mutane suka ɗan tarun nan yau sai naje har can sai ki isoni da keken".
Cikin mamaki tace
"Notyart zaka iya, da nisafa".
kanshi ya jinjina mata tare da cewa.
"Karki damu in sha Allah zan iya".
Kai ta jinjina mishi.
alamar to shi kuwa miƙewa yayi a hankali ya fara taku yana tafiya a .
Ita kuwa ido ta zuba mishi da cikinta da yanzu ya cika wata biyar ya fito ras a gabanta.
ya daɗe kafin ya isa wurin da yace ɗin yana isa yaji tana mishi tafi tare da cewa.
"Alhamdulillah Nooryart am hoini".
Da sauri ta fara turo keken har ta iso gabanshi,
tana isa ya zauna tare da sauƙe ajiyan zuciya cikin fidda numfashi yace.
"Kai na ɗan gaji kam".
Sunkuyowa tayi ta ɗanyi kissing goshinsa.
tana ɗagowa kuwa taji anayi musu tafi,
sabida wasu sun lura mara lfya ne,
hannu sukayi ta bawa Saifuddeen suna mishi fatan lfy.
A haka sukaci gaba da tafiya har suka ratso, kan Buzy Turkish street.
Da sauri Zaleeha ta riƙo hannunshi tare da cewa.
"Laaa Hamma Saif kalli can suna gasa masara, muje ka saya min zanci gashesshen masara".
Da sauri ya kalli inda take nuna mishin. Tabbas ɗanyar masara wani ke gasawa a ɗan wani ƙarfe da akayi kamar tukuban gashin tsirai, matane ke ɗan tsastsaye suna saya,
ido ya lumshe mata tare da cewa.
"Muje in saya miki a cicina rumbun gwamnati".
Baki ta ɗan tura shi kuma hannunta yaja suka isa wurin.
Ganinshi bisa kekenshi ne yasa a take aka basu hanya suka isa suka saya ba tare da bin layiba, saida suka isanema sukaga ashe harda dafaffiyar gyaɗa ai kuwa shima sun saya.
Gefe suka ɗan yi inda ake saida abubuwa sauran kayan ciye ciye suka saya, shike riƙe da ledar tana biye dashi a baya.
Suna ɗan dube-duben wurinda zasu zauna su ɗan hutane kuma Zaleeha ta hango mai saida su inabi da tupa,
nan tasa masa daru kan cewa ita lallai saitaci inabi da tupan, shida kansa ya taka da ƙafafunsa inda yaje ya saya musu inabin da tuppan, har yaje sayo ya dawo vedio take masa.

Yana dawowa ya zauna tare da nuna mata saibot ɗin wani babban wurin hutawa.
Nan suka kama hanyar tafiya kaɗan sukayi sai gasu
cikin wani gurin shaƙatawa na Goztepe 60th year park, wurin mai tarihi da kyau.
Acan sukaci masaran dama duk abun ƙwalaman da suka sayo. Sunjima awajen shaƙatawan sai shawagi suke ananne kuma ya dage wajen tattaka ƙafansa, sai wajen yamma gab magriba

sannan suka kira direbanshi yazo ya ɗauke su suka koma masauƙinsu,  atare sukayi wanka, yayinda tundaga cikin toilet ɗin labari ya sanja salo, sosai suka sha love dinsu acikin bathroom ɗin, yauma haka ya dinga mata sambatu irin wanda bata gane me yake faɗaba, dan itama fitar da ita daga hayyacinta yake.

Sosai suka gajiyar da kansu hakanne ma ko sallan Magriba agida yayi, inda ya jasu jam'i, suna idar da sallan Isha kuwa sai bacci, sai washe gari da safe ne ya ƙira su Ummi suka gaisa, jin suna gaisawa da Ummi ne yasa Zaleeha ta karɓi wayan suka gaisa, bayan sun yi sallama da Ummin ne ta ƙira wayan Hayatuddeen saboda da da sukayi waya da  Ummi basu samu daman gaisawa ba, saboda yana makaranta, koda ya ɗaga wayan kuwa hira suka sha sosai, kasancewar suna tare da Zakariyya, yasa ya bawa Zakariyya wayan suka gaisa,  bayan ta gama  waya dasu Zakariyyan Ziyada ta ƙira suka sha hiransu.             Taji daɗin yanda taji muryan Ziyadan dan da dukkan alama tana samun jindadi da kulawa daga wajen Yaya Ameenu yadda ya kamata, ko dama tasan ya Ameenu zafinshi baya kan matarshi, don ko ita kanta tana mmkin yadda ya zama kamar bawa ga Adda Maryam sai dai in tayi duba da yadda Adda Maryam ke biyeyya a gareshi sai tace ta canci ya mata komai ma, to kuma tasan Ziyada ma irin Adda Maryam ɗince.                Yau ma dai basu wuni agida ba, dan ma saidare sannan suka dawo masauƙinsu, tundaga ranar kuwa yawanci kullum sai sun fita , kullum cikin yawon zuwa wajen shaƙawata suke, Alhmdulillahi kuma zuwa yanzu Ƙafar Saifuddeen tana ci gaba da zama normal.

*******

Alhamdulillah yau watansu biyu da sati uku, da zuwansu Instanbul yayinda cikin Zaleeha ya kusa cika watanni bakwai ras.
Yau ya kama saura sati guda kenan su koma Nigeria,  acikin watannin da suka shuɗe ɗinne kuma, Zaleeha ta fara zuwa awu nan cikin wani babban asibitin Acibadem Hastanesi Hospital instanbul.
Dake Cikin tsakiyar birnin  Instanbull, asibitine me kyaun gaske da tsaruwa komai cikin ci gaba da gwarwa suke mata auwan cikinta da bata dukkan kulawa da shawarwarin yadda zata kula da kanta da cikin dake jikinta.
Sannan kuma acikin watannin  sosai sukaji dadin rayuwarsu a Instanbull,
kulawa me tsabta suke bawa juna, shaƙuwarsu ta ƙaru, kodayaushe suna jikin juna suna tattalin cinsu, duk randa akayi dusar ƙanƙara kuwa zama na musamman Hamma Saif yake ta buɗe mishi tirtsetsen cikinsu ya ɗun-ɗuma musu abinda ke ciki daga nan kuma wasa ke sauya salo.

Zuwa yanzu kuwa Saifuddeen yana tsayawa akan ƙafafunsa car, tafiya kuwa babu inda baya zuwa,  hakanne yasa shi jingine wheelchair ɗinsa, da ƙafafunsa suke fita suje yawonsu su dawo,   wata irin zazzafar soyayyace ta shiga tsakaninsa da Zaleeha me wuyar fassaruwa, acikin ƴan watannin kowanne yasan sirrin kowa, sun zama kaman wasu shaƙiƙan abokai, acikin watannin kuwa kullum sai sunyi waya dasu Ummi, kuma tana ƙoƙarin ƙiran Mama da kuma Mamy harma da Baba Malam da Ziyada, sosai sukejin daɗi, musamman ma Baba Malam da

ayanzu yake al'fahari da ita Ummi yanzu ta fara cewa suyi maza su dawo wai kada Zaleeha ta haihu a wannan ƙasar sanyi ya kama mata jiki, Saifuddeen kanyi dariya yace.
"Ummi cikin tai wata bakwai ne".
Takan ce to ba Ameena bakwaini ta haihuba waya sani ko daga gunshine Zaleeha bakwaini zata haifa yanayi dariya yace mata, a a Ummi shi wannan taranni za'a hafo in sha Allah da haka dai suyita hiran cikin suna dariya, Raliya kuwa har cewa take Zaleeha tayi hoton cikin ta turo mata shike hanawa yace ta bari sai sun dawo, Ameena kuwa yanzu ce mishi take itafa ta tayi ƙewarsa daga nan yaita mata tsiya yace ta shirya duk randa ya dawo zai bata ajiyan ƙanwar Adeel.

Yauma shirya kansu sukayi cikin kayan sanyi, suna riƙe da hannun juna haka suka fito daga cikin hotel ɗin.
Wani Garden sukaje suka ɗan shaƙata, tare dayin hotuna masu kyau wani a tsaye wasu a zaune wasuma suna kunce cikin korayen shuke-shuken wurin wani a bakin ruwa, kuma duk hoton da zasuyi sosai cikin Zaleeha ke fitowa tim a gabanta, wani hoton da sukayi.
yana zaune ya mike ƙafa ita kuma tana konce tayi pillow da cinyoyinshi, hannunshi ɗaya na kan cikinta ɗaya na kan goshinta, yana murmushi tana murmushi sosai sukayi masifar kyau a hoton sun daɗe sosai a ciki kafin suka fito suka nufi masaukinsu.

Ahanyarsu ta dawowa ne suka biyo kusa da asibitin da Zaleehan ke awu, anan Saifuddeen ke tuna mata cewa.
"Mu dear Gobe nefa dawowanki awu".
Kai ta gyaɗa masa alaman ta sani, murmushi yayi tare da kamo kafaɗunta, cikin kulawa yace.
"Karki damu Insha Allah gobe zan tashi da wuri saina rakoki kinji, duk dama dai kinƙi amiki scanning, bansan daliliba kuma".
Ɗan shagwaɓe fuska tayi akasalance tace.
"To Hamma Saif bagani ba lafiyata ƙalau, scanning ɗin me zanyi, duk abinda zamu haifa zamu ganshi randa ya fito duniya, naga ɗokinka yawane dashi".
Hannunshin yasa ya ɗan shafi cikin tare da cewa.
"Ai basai baki da lafiya za amiki scanning ba, yanzu fa cikinki yayi girma kusan 7 month ake nema, bakya ganin yanda yayi girma da yawa, maybe ma ƴan huɗu zaki haifamin ƴar al'barka".
Idanunta taɗan zazzaro, sai kuma ta saki murmushi tare da lafewa ajikinsa.
Shi kuma murmushi yayi a ransa yace.
"Tun yaushema akayi scaninng ɗin, duk dai bawai nayi imani da abinda sukace ba, amman bazan ce miki komaiba zanyi ta miki addu'a Allah ya sauke min ke lfy".
Ahaka suka koma gida, bayan ya saya mata kayan ciye ciye.
Daren yau ma dai soyayyarsu suka sha, yau abun na Saifuddeen harda kukan dadi, dan kullum sabuwa Zaleehan ke zame masa kodan dama ɗan-ɗanon mai ciki na dabanne, shiyasa akullum yake zaucewa akanta.
Washe gari kuwa kaman yanda ya faɗa, yau da wuri suka tashi, shida kansa ya shiryata dan zuwa yanzu bakomai take iya yi da kanta ba, saboda yanda cikinta yayi girma, idan bakasan watannin cikin ba zaka iya cewa ya cika wata tara.
Har cikin asibitin ya kaita aka mata awu da duk wasu gwaje gwajen da suka dace, suna cikin

asibitin kuwa aka soma yi musu dusan dusan ƙanƙara,   yanda ta matsa masa cewar tanajin yunwa ne yasa dole suka bar cikin asibitin,
wani restaurant dake kusa da asibitin suka nufa, kafun ma su ƙarasa tuni dusan ƙanƙara  ya sauƙa ajikinsu suna shiga cikin. Kasibeyaz Florya Restaurant.
  Abinci me rai da lafiya sukaci acikin restaurant ɗin kana suka sha zazzafan tea mgnin sanyi, yau basu wani ɓata lokaci awaje ba suka koma masauƙinsu.

 bayan sunyi sallan Ishane Saifuddeen ya ƙira Ummi vedio call, inda ya saita vedion  har Zaleeha dake gefensa ma tana hango Ummin, hira sukayi sosai kaman suna gida, dan har Hayatuddeen saida yazo sukayi hira.

Bayan sunyi sallama ne, Saifuddeen din yayi musu connecting game suka soma yi, ahaka bacci ya ɗaukesu dukansu.

Wayewan garin yau kuwa basu fita ko ina ba agida suka zauna,  Zaleeha kuwa sai faman zuba masa raki take, tana masa mitar cewa cikin na mata nauyi, shi kam tarairayanta kawai yake.
Haka dai suka shafe kwana huɗu basu fita wani yawo me tsawo ba sabida sosai cikin Zaleeha ya girma, aranan da ya rage saura kwana uku su koma Nigeria ne, suka shiga wani babban super market,     dake kan  Cobblestone street instanbul.
Sayayya sukayi sosai harda na ban mamaki, dan Zaleeha ita kanta saida tasha mamakin yanda yayi ɓarin dukia wajen sayan kayan babies,    har saida ta kasa haƙuri cikin gajiya tace.
"Hamma Saif kayannan sunyi yawa, me zamuyi dashi? sai kace wanda zan haifi ƴaƴa dozin dozin, gaskiya arage sunyi yawa over".    Batare da ya yarda sun rage kayan babies ɗinba yace.
"Kikasani ko dozin-dozin zaki haifa mana".      Hararan wasa tayi masa tare da cewa.
"Chab ai kuwa ni ba ingine bane."
  Dariya yayi, sannan ya ci gaba da ɗaukan abun da yake so, tare da cewa.
"Ni kam ingine yara dozin-dozin na zuba miki, kin san dai NAKASA BA KASAWA BACE". dariya tayi tare da cewa.
"Na yarda Nooryart na sani wlh NAKASA Ba KASAWA BACE, ni kam ai ni naga zahiri tunda a nakashen aka amshe budurcin harda sumar dani sau biyu, ga ɗan karen naci".
Signal ya mata da girarshi ɗaya kana ya lakaci hancinta sannan sukaci gaba da sayayya,
 kaya suka saya niƙi niƙi.

Bayan sun gama sayan duk abinda suke sone  Hamma Saif ɗin ya ƙira ɗaya daga cikin ma aikatan hotel ɗin wanda suke da motocin taxi,  bajimawa kuwa yazo ya kwashesu da kayansu ya maidasu masauƙin su.

Gombe Nigeria.              Hayatuddeen ne keta faman shirya kansa, cikin riga da wandon tsadaddiyar shadda, yayi kyau matuƙa gashi ya murza hula me kyau akansa, kallon kansa yayi amadubi, murmushi ya sake dan ganin yanda yayi kyau.
Ɗan makullin motar  dake ɗaya daga cikin motocin Hamma Saif wanda ayanzu shike amfani da

ita ya ɗauka, afalo ya samu Ummi da Raleeya, ganin yanda yayi kyau yasa Ummi cewa.
"Masha Allah Autana kaga yanda kayi kyau kuwa, sai ina haka?". Wani irin sanyi yaji aransa, sakamakon jin Umminsa ta yabesa. Kansa yaɗan sosa, cikin ƙasa da murya yace.
"Ummi gidan Baba Bello fa zanje, na kai masa gaisuwa amadadin Hammana kinsan yau jumma'a".
Murmushi Ummi tayi cike da jin daɗi tace.
"Masha Allah to adawo lafiya, hakan yana da kyau sosai ai, maza kace musu ina gaishesu."
Cikin jin dadi yace. "Insha Allah Ummina zan faɗa musu."
Kallon Raleeya yayi cikin tsokana yace.
"Adda Raleey how far naga baki taya ba, kodai kina baƙinciki da kyawun da nayi ne, dan kinga nafi Ya Ahmad kyau". Hararan wasa Raleeya ta watsa masa, kwafa tayi tare da cewa.
"Oho kadai ɗanyi kyau kaɗan. Amman ko rabin ya Ahmad bakayi ba a kyau yaro, daga Hamma Saif sai Ya Ahmad a kyau".
Murmushi kawai yayi, sannan ya fice daga cikin falon.
Yana zuwa ya shiga motarsa, kai tsaye gidan Baba Bello ya nufa, aƙofar gida ya taradda Baba Bello'n, da alama fita zaiyi, bayan sun gaisane yake tambayan Baba Bello'n, ina zaije?".
Nan Baba Bellon ke cemasa zaije gaishe da ƙanwarsa ne wato Maman Zarah, saboda kwana biyu bata ji daɗi ba mura ke damunta, wani sanyi yaji aransa jin cewa Baba Bellon gidansu Zarah'nsa zaije, nan take yacewa Baba Bellon ya shigo motan ya kaisa.
Hakan kuwa akayi, saidai koda sukaje gidan, bayan ya sauƙe baba Bellon, cewa yayi shima zaije ya gaishe da Maman Zarah'n, sosai kuwa Baba Bello yaji daɗin haka, saida sukasa aka musu iso, sannan suka shiga cikin gidan. Ababban falon gidan suka zauna.

Cikin nutsuwa kuwa Zarah ta shigo hannunta ɗauke da tray wanda ke ɗauke da ruwa asamansa.
Agabansu ta ajiye, cikin girmamawa ta gaishe da Kawun nata, fuska asake Baba Bello ya Amsa mata,
ganin idon Baba Bello'n yasa ta gaishe da Hayatuddeen saidai bata yarda ta kalleshi ba.
Amaimakon ya amsa mata gaisuwan nata, sai ya gyara zamansa tare da cewa.
"Meyasa wayan baya shiga, always idan nakira baya tafiya, meyasa?". Ƙin amsa masa tayi, asanyaye ta juya zata bar falon, cikin ƙara jadda da mata yace.
"Badake nake magana ba, me yasa wayar bata shiga".
Ɗan ƙaramin bakinta ta ɗan tura, cikin ƙasa da murya tace.
"Sace wayan akayi." Batajira ya sake cewa komai ba ta juya cikin sauri tabar falon. Dai-dai lokacin kuwa Mamanta ta fito, amatuƙar ladabce ya gaishe da matar, wanda take da kwarjini, fuska asake kuwa ta amsa masa, tana me yaba haibansa, dan kallo ɗaya zaka masa kasan cewa yaro ne, amma kuma akwai cikar haiba da hankali, ga girmama na gaba ga nitsuwar. Da bata gane aro nitsuwar yayiba,
Shi kuwa Hayatuddeen sosai ya danne rawan kanshi ya nitsu a gaban surkarsa a gaba in Allah ya nufa.
Bayan ya gaishetane ya tashi ya fita, bayan sunyi da Baba Bello cewar zai jirasa amota.

Turkey Instanbul. Yau ya rage saura kwana ɗaya rak su

koma Nigeria, hakan ne yasa suka sake fita zaga gari, wani park me kyau sukaje inda suka yi hotuna masu kyau, take kuwa ta watsasu ashafinta na IG da kuma Whatsapp status ɗinta. Kowa ya gani kuwa sai ya mata comment, dan sunyi kyau matuƙa.    Bayan sun dawo gidane Saifuddeen ya maƙale mata kaman ƙaramin yaro, yau sosai ya jigata ta, har saida tayi laushi kafun ya barta, ihu da sambatu kuwa ta shashu, har mamakinsa take dan abun nasa kullum gaba gaba yake, matuƙar zaiyi sex da ita to sai yayi ihu da kukan daɗi, gashi ko da yaushe jarabansa ƙaruwa take.

Washegari da safe ƙarfe 8 dai-dai jirginsu ya tashi daga ƙasar ta Turkey zuwa Nigeria sosai taji kewa da begen ƙasar hakanan taji kamar tace su koma su ƙara wata biyu a nan sabida zamansu a garin wani sashine na daɗin tarihin rayuwarsu.
kafun su tashine kuma sukayi waya dasu Ummi, inda suka ƙara musu 1 hour akan lokacin da zasu iso, dan so suke su musu surprise.

Ko acikin jirgi liƙe suke da juna, gwanin ban sha'awa.
Sukansu basu san wani lokaci suka ɗauka suna keta hazo ba, suna cikin mood me daɗi jirginsu ya sauƙa acikin garin Lagos Nigeria, lokacin da suka fito daga cikin jirgin, saida suka sauƙe zazzafan ajiyar zuciya, tabbas sunyi kewar ƙasarsu ga wani ɗumi da sukaji ya ratsosu saɓanin sanyin da suka baro, kasancewar sunyi booking flight ɗin da zai kaisu Gombe, yasa basu wani jima a airport ɗin ba jirginsu ya ɗaga zusa Gombe.
Lokacin da jirginsu ya sauƙa acikin garin Gombe wani irin dadi sukaji acikin ransu, tabbas kowa yabar gida gida ya barshi, komai rashin dadin naka naka ne, lallai ko ina kaje da ka dawo tushenka, zakaji wani irin sanyi da salama acikin ranka wannan shine tunanin da sukeyi a lokacin da suke taka steps ɗin jirgin suna sauƙa.
Taxi suka nema, Saifuddeen ne ya gaya masa unguwar da zai kaisu sannan suka kama hanya.

Acan gidansu Saifuddeen din kuwa, yau zuciyoyinsu cike suke da farincikin dawowan su Saifuddeen ɗin, dan hakane ma Ameena ta kashe zuwa aikinta na yau, da kanta tashiga kitchine, ta haɗa musu abinci me rai da lafiya, bayan tagama ko ta caɓa ado, anna falon Ummi suka zauna dukansu hadda su Adda Rahama, jira suke lokacin dasu Saifuddeen ɗin zasu iso suje su tarosu.

Can waje kuwa adai-dai ƙofar gidan nasu kuwa me taxi ɗin ya sauƙesu.    Sule driver wanda dawowansa daga masallaci kenan, ganin Ogansa tsaye akan ƙafafunsa yasha mamaki ƙwarai ya kuma yi murna sosai, harda ƙwalla saida yayi.
Shiya shiga kwasna kayan su Saifuddeen yana kaiwa cikin gida can side ɗinsu kamar yadda ubangidashin ya umarce sa.

Shikuwa Saifuddeen yana sarƙe da hannun Zaleeha suka nufi part ɗin Ummi sabida yasan in Ummi taga ana shiga da kayansu zata fito, shiko yafi son ya shiga har ciki ya samesu yaga irin farin cikin da zasuyi.

Abakin ƙofar shiga falon suka tsaya, Zaleeha ne tayi masa alaman cewar ya fara shiga, hakan kuwa akayi ahankali ya murɗa handle ɗin ƙofar ya shiga da wani irin taku mai cike da haiba tafiyarsa irin ta RK ta fito ras bakinsa ɗauke da sallama ya shiga.
Jin sallaman sane yasa dukaninsu suka jujjuyo da sauri.
Ganinsa tsaye akan ƙafafunsa yana sakar musu murmushi Yasa su Raleeya da Hayatuddeen fasa wani uban ihu, da wani irin gudu sukaje suka faɗa jikinsa, Ummi da Adda Rahama da kuma Ameena da Ahmad kuwa cikin tsananin farin ciki suka mimmiƙe tsaye cike da zallan mamaki da al'ajabi da kaɗuwa, sukace.
"Lahh hauwalaƙuwata illabih, Alhamdulillah".
sosai suka shiga shock ɗinn ganinsa, wani irin matsanancin farinciki ya cika zuciyarsu, har hakan yajawo taruwan ƙwalla acikin idanunsu. Cikin matsanancin farinciki Ummi ta durƙushe a wurin ta fuskanci gabas sujjadar godiya tayi wa mahaliccinmu ,
kana ta miƙe da jiki na rawa tace. "Alhamdulillah! Alhamdulillah!! Alhamdulillah!!! Babana kaine kuwa kai nake gani tsaye akan ƙafafunka? Alhamdulillah ko yau ko yau na koma ga mahaliccina burina da fatana da addu'a ta sun ciki, Allah na gode maka yau bani da sauran damuwa a duniya a kan wannan ɗan nawa bawanta mai rauni".
Shi kuwa Saifuddeen da sauri ya ɗan janye su Raleeya daga jikinsa yayi cikin matsanancin kewan Ummin nasa ya ƙaraso cikin falon haɗasu yayi dukansu biyu, wato Ummi da Adda Rahama da ta zama kamar an dasata ya rungumesu ƙam, cikin farinciki yace. "Nine Ummi Saifuddeen dinki ne, Allah yayi ikonsa na warke tun bamu jima da xuwa Instanbul ba, na ɓoye muku ne saboda ina matuƙar so nayi surprising ɗinku sabida ina son ganin wannan farin cikin naku da nake gani yanzu ido da ido." Murmushi Ummi tayi tare da rungumesa ƙam, wani irin tarin farinciki takeji acikin zuciyarta, sosai ranta yayi sanyi, tabbas wannan rana zata shiga cikin ranaku mafi girma na rayuwarta, yana rungume da Ummin ya kashewa Ameena idanu, wanda tun ɗazu kallonsa take tama kasa ɗauke idanunta daga kansa, saboda ba ƙaramin kyau ya ƙara ba, yayi fresh har ɗan ƙiba yayi, da'alama babu wani abun dake damunshi ga tarin farin cikin ganinsa a tsaye ji take kamar ta ture Adda Rahma ta gurbinta a jikinshi.
Zaleeha ce wanda shigowarta falon kenan, cikin sakalci da tura baki tace.
"Wayyo Allah na, dana sani da ban amince maka akan maganan surprising ɗinnan ba, tun da dai gashi kai kaɗai kawai aketa kulawa nikam kamar ba a sanni ba an mance dani".
Maganar da takeyi ne yasa gaba ɗaya hankalinsu ya dawo kanta.
Raleeyace ta rungume ta cikin farinciki tace. "Oyoyo my aunty, i miss you more".
Murmushi tayi itama ta rungume Raleeya, ahaka suka ƙaraso cikin falon, daga kan Ummi har zuwa Ameena saida duk ta bi ta rungumesu, sosai suka yaba da irin zallan kyawun da tayi, duk da cikinta ya ƙara girma, haka ma hips ɗinta sun sake cikowa, ta zama wata babbar mace, ta kara zama cikakkiya abun so ga ko wani namiji.
Anan falon suka zazzauna, suna ahaka kuwa su Ishaq da Mudassir da kuma Salisu dama su Wareesu suka ƙaraso domin Ibrin isowarsu da Ahmad ya basu da workewanshi, baƙaramin murna suma sukayi da ganinsa ba, daɗi kam sunjisa alokacin da suka ga yana taka ƙafafunsa.
Hira sukayi sosai a falon Ummi da aminanshi sunyi farin ciki mai tarin yawa anan a take yake cewa Ishaq ya shirya nanda wata biyu shida Rashida zasu tafi India ganin likitan ido, nan duk akayi ta fatan Allah yasa shima a dace, daga nan suka cicci abin gwalamar da Ameena tai musu, sannan suka fito suka nufi cikin Garden ɗin dake bayan part ɗin Ummi dan su ɗan barshi

ya gana da iyalansa saida suka fitan.

kafun shida Zaleeha kowa ya nufi sashinsa danyin wanka, ita part dinta ta wuce wanda Zahira da Ziyada da Raliya suka gyara matashi fes-fes.

Shi kuwa ƙiran Ameena yayi yace tazo ta haɗa masa ruwan wanka.

Suna shiga part ɗinsa ya jawota jikinsa ya rungumeta ƙam, anutse ya shiga kissing ɗinta tako ta ina, tare da ce mata.
"I miss You so much cingom ɗina".
biye masa tayi dan itama tayi missing ɗinsa sosai, wata uku cur batare dashi ba ji take kaman shekara uku ne, cikin tsananin jin daɗi tace.
"Miss You too ya Habibi". saida sukayi tsotse-tsotsen su sannan yayi wanka.

Afalon Ummi suka sake haɗuwa, nan cikin falon suka baje, anan sukayi ciye ciyensu.
Haka sukayi ta hira, sai da aka ƙira sallan magriba sannan kowa yaje yayi sallah.

Su Ishaq basu bar gidan ba sai bayan sallan Isha, haka suka dai sha hiransu, ƙarfe tara kuwa kowa ya nufi part ɗinsa, Zaleeha kam sanin cewa ba itace ke dashi ba yasa ta na kwanciya se bacci dan agajiye take jin kanta.

Shida Ameena kuwa nan cikin bedroom ɗinsa suka ƙule, cikin aminci da salama suka raya daren nasu, inda Saifuddeen ya dage ƙwarai wajen nuna mata yayi missing ɗinta, sosai ya jiyar da ita daɗin dayasa ta kuka, haka suka liƙewa juna har kusan ƙarfe 1 na dare. Saida suka gurji juna sosai kafun suka kwanta.
Washe gari kuwa Bappa Ali ne yazo ya duba Saifuddeen ɗin ya ji daɗin ganin Saifuddeen ɗin na tafiya ƙwarai, haka dai suka wuni yau ɗin cikin nishaɗi, mutane sai zuwa musu barka ake, ƴan uwa da abokan arziki su Alhaji Rabi'u dasu Baba Bellon da Alhaji Yawale da Alhaji Kabiru da dai duk manyan yan kasuwa da mutanen wajen aikinsu.
Ya Ameenu ma da Ziyada sun zo.
Hakama da daren Baba Malam da Mamy da Mama sun zo, Ya Ahmad kuwa kiranshi yayin waya ya mishi barka, Aunty Kubra ma tazo haka Rashida da Umman Ishaq hakama Jabeer da Hisham suma sunzo da matansu a daren.

Koda suka shga kuwa Saifuddeen da Ameena kamar zasu cinye juna. Adeel kuwa kam ya maƙalewa Zaleeha ranar tare suka kwana sabida Ameena tace mata yanzu baya tashi shan nonon dare.

Washe gari kan Zaleeha zata amshi miji tace a a ita kam ta yafe mishi yaje suyi sati ɗaya rak da Ameena ita zata raini cikinta ta huta da gurzan data sha a instanbul.

Randa ta cika satine.
Washe gari kuwa Zaleeha ta amshi girki, da dare haka suka shana ita da Saifuddeen dan hutun

satin da suka samu duk sunyi mararin juna, sabida ita kanta soyayyar tana bukatar hutu bare kuma aurataiya.
Bayan dawowansu da kwana goma cib.
A ranar ne  kuma  ƙauran su Raleeya,    babu yanda Zaleeha batayi da Ahmad ba akan ya bari sai bayan ta haihu sannan su  ƙaura,   murmushi yayi tare da cewa.
"Chab naƙi wayon, hakanan sai na bar matata kuta samin ita bauta ko yaushe tana kitchen kamar ƴar aikinku ita ba haihuwa ita ba karatuba ita ba hutun bautaba ita ba gidan mijiba ai abin ya mata yawa, gaskiya na gaji inason matata ta huta, hakanan kullum fa ita ke muku girki, amma dai namiki alƙawari idan kika haihu zamu zo muyi sati, tun da ai muna da ɗaki agidan nan".
   Dariya duka falon sukayi, dan su kansu sunsan Raleeya na aikatuwa ƙwarai.

Bayan sun gama kimtsa komai ne, da yamma dukansu suka raka Raleeyan zuwa haɗaɗɗen gidansu da Ahmad ya ƙenƙesa musu, Ummi kaɗai suka bari agidan, dan har Saifuddeen saida ya raka ƴar ƙanwar tasa, sosai gidan nasu yayi kyau sashin su mai girman sai BQ da kuma Sashin Gogga Dada Baba. Wanda tuni an kwaso musu komai nasu, suma har Sule ya tafi ɗaukosu.

Anan sukayi diner sai dare suka dawo.
 washegari kuma Ummi da ta raka Goggo Dada da mijinta tanayi misu tsiya wai sun zama amare.
Kana da yammacin ranar kuwa aka kawowa Ummi ƙanwarta me taimaka mata aiki gida, wanda take ƴar Baffan Ummin dake gari Hashidu ƴar iya Bukku, to kasan cewar iya bukkun ta rasu yanzu zumunci sukeyi sosa,  kasancewar tana da matsalan jinnu shiyasa har yanzu batayi aure ba,    tana da hankali kuma ƙwarai, uwa uba tsabta, sannan ta iya girki, duk wani abu da bata gane ba kuwa Ummi take tambaya ta ganar da ita,
Kana dama Ummi da kanta ta sayi ɗan ƙaramin gida ta dawo da Baffa nata nan ta kuna bashi kuɗin aure ya auro wata tsohuwa mai kirki, daga nan suka dawo cikin gombe da Goggonta Goggo Abu da bata taɓa haihuwa nan ba.
Yaran baffa nata kuma maza duk suna can garin Hashidun, koda ta gayawa Saifuddeen abinda tai cewa yayi ai shima dama yanada niyar dawo dasu nan dan haka ya maida mata kuɗinta, ita kuma Ummi taƙi amsa tace a a tayiwa ƙanin mahaifin ta kyauta da arziƙinta.

Zaleeha kuwa yanzu cikinta yayi girman da yake basu mamaki,    hakanne yasa duk suke tattalinta.
Yanzuma zaune take akan sofa inda ta mimmiƙe ƙafafunta, kanta kuwa na kan cinyar Saifuddeen dake zaune akan kujera, hannayensa duka na cikin gashin kanta yana shafawa. Ɗago kai tayi ta dubesa tare da cewa.
"Honey  wai ya batun aikina ne, har yanzu bakace komai ba, gashi kuma har yanzu baka bani motata ba,  saidai idan zan fita na karɓi motan aro".
Murmushi yayi tare da sauƙowa ya zauna akusa da ita, cikin kulawa yace. "Motocinki duka biyu sunananan idan bakya sonsu ma sai nasanja miki wasu, naga motar Ummu Adeel ma taɗan tsufa inason sanja mata sabuwa,  idan na tashi zan sanja muku tare, wace iri kikeso?."

Ɗan fari da idanunta tayi, cikin salon tsokana tace.   "Range rover nakeso". Dariya yayi tare da cewa.  "Kinaganin bazan iya saya miki ita bane?."    Kai ta girgiza tare da cewa.
"Ba haka nake nufi ba, ai nasan kaiɗin  babban mutum ne".
 Kansa ya jinjina tare da cewa.
"Inma zugani kikesonyi to na ɗauka, saboda haka kushiryawa ganin sabbin Range Rover, maganan aikin ki kuma ki bari sai kin haihu kafun nan ƴaƴan mu sun ɗan ƙara ƙwari, sai ki koma kinji ko."    Cikin jin daɗi ta rungumesa tare da manna masa kiss agoshinsa, cike da farinciki tace.
"Thank you Mijina ɗan al'janna".
   Dariya yayi sannan suka ci gaba da hiransu.

Bayan dawowansu da wata biyune kuwa Ishaq da Imran da Rashida suka tafi India dan ganin likitan ido.

Kwanci tashi ba wuya  rayuwa tayiwa familyn daɗi sosai,    inda yanzu cikin Zaleeha ya cika wata takwas da sati biyu, sosai cikin ya ƙara girma, zama da ƙyar tashi da ƙyar,  ƙafafunta kuwa sun kumbura sosai, hakanne ma yasa kusan kullum asashin Ummi take wuni, dan Ummi ce dakanta keyi mata komai, kasancewar yanzu Saifuddeen ya tsaya akan aikinsa sosai, kullum da safe sai ya fita office, idan yazo dawowa kuwa saiya cikowa Zaleehan leda dakayan ciye ciye, dangin fruits da kuma chocolates.

Anan hakanne ya biya musu zuwa umra, duka gidan baki ɗaya, harta  Ahmad da Raleeya ya biya musu, haka ma Hayatuddeen da Zakariyya, sai su Sameenu da Raihana da kuma Wareesu Wasilanshi harma da Saleesu, Safiya shi sannan Mudassir da Muminai shi, sai Adda Rahma da Ya Adnan ɗin shi.
Kana can gefensu Zaleeha kuwa Ya Ahmad ya biya Mamy da kuwa Ziyada da Habu, haka yasa Ya Ameenu yace to shima zaije baza'a barshi shi ɗaya a gidaba.
 duka abokansa babu wanda be biyawa ba, har ma Baba Bello  da Iyya saida ya biya musu dasu Goggo dada.
yaso suje tare dasu Ishaq sai-dai zuwa lokacin shida Rashidan sa sunyi sati biyuma da tafiyarsu India,   sai kuma Ameena wanda itama bazata samu zuwa ba, kasancewar awajen aikinta ba abata dama ba, sannan kuma babba ma dalilin idan suka tafi dukansu zai zamana gidan nasu ba kowa,  hakanne yasa tace ta haƙura wani zuwan Insha Allah sai aje da ita.  A ranta kuma tafi son taje daga ita sai mijinta.

 Haka dai ranan wata jumma'a jirginsu ya ɗaga zuwa sararin samaniya.

Basu sauƙa ako ina ba kuwa sai a ƙasa me tsarki.
Suna zuwa kuwa suka fara gudanar da ibada, sosai suka nutsu sukayi ibadansu me kyau yayinda gaba ɗayansu Saifuddeen keta binsu da roƙon susa mishi Zaleeha a addu'o'in su ,
Allah ya sauƙeta lfy, haka kuwa akayi gaba ɗaya su suna sata a addu'o'insu.

Aranan da suka cika kwana goma da zuwa ne,  Da sanyin safiya naƙuda ya tashi wa Zaleeha, abu kaman wasa sai gashi ya kan kama, domin sosai bayanta ya riƙe, tun tana daurewa tana cijewa ita ɗaya har dai ta gaza, kasan cewar masauƙinsu a jere-a jere yake,
cikin dauriya ta nufi inda Ummi da Mamy suke,
tana shiga da tasu mamy na sa kaya, Ummi kuwa tana bathroom tana wonka da alamun zasu tafi haramine.
Mamy na ganinta da yadda take tafiya tace.
"Zaleeha lafiya kuwa?".
Da sauri Mamy tayi kanta ganin yadda take ɗaga ƙafarta da ker sabida sauƙowa daga sama da tayi ya tunzuro naƙudar,
cikin rawan murya tace.
"Mamy marata bayana ƙuguna".
Cikin kaɗuwa Mamy tace.
"Hasbunallahiwani'imanwakil kodai haihuwace?".
Dai-dai lokacin kuwa Ummi ta fito cikin kaɗuwa tayi kansu,
ganin yadda gaba ɗaya taketa tsastsafo zufa ne yasa Ummi cewa.
"Haihuwane Mamyn Ahmad kira mana yaran mazan".
Sai ta kuma kamo hannu da Zaleeha ta soma yarfa hannuwanta, da cije baki, ganin hakane yasa hankalin su Ummi tashi.
Cikin gigita Ummi ta lalubi wayarta ta kira Saifuddeen wanda shi kuma lokacin suke dawowa daga harami shida Dr Adnan da kuma Salisu.
ganin sun isone yasa bai ɗaga kiran Ummi ba kawai ya nufi ɗakinsu.
Da sauri ya ƙaraso cikin ɗakin a kuɗine yace.
"Ummi meya sameta, Zaleeha meke miki ciwo?".
Da sauri Mamy ta ɗan matsa fahimtar itace ta hanashi ƙarasowa,
ai kuwa tana matsawa ya tallabo Zaleeha,
Ummi kuwa hijabi tasa bayan tasa riga cikin fargaba tace.
"Haihuwane Saifuddeen mu tafi asibiti".
Saifuddeen da kansa ya ɗagata  caɗak  nufi hanyar fita Ummi da Mamy na biye dashi.
Suna fitowa Ya Adnan na saukowa ganin halin da suke ciki yasa maza ya koma ɗakinsu takardun awun Zaleeha na Instanbul dana Nigeria ya kwaso wanda a hasashen duk sukaga wai yara biyune a cikin Zaleeha amman ɗayan kawunanshi biyu,
wannan dalilin ne ya tashi hankali Saifuddeen shiyasa ya biya musu Umrah baki ɗaya dan su tayashi addu'o'in samun waraka a lamarin, haka yasa daga nan F.M.C Gombe sukayi musu takardar transfer zuwa nan asibitin saudia,
Suna fitowa suka samu Samisu ya dawo, so a motar daya dawo suka tsaida.
Bayan ya sata amota, ummi ne ta rufa musu baya sai kuma su Mamy da  Raleeya.
Suna kaita asibiti kuwa Doctors suka karɓeta da gaggawa ganin abinda ke kan takardunta, da sauri aka wuce da ita labour room.
Gaba ɗaya Saifuddeen rikicewa yayi, dan ya kasa control ɗin kansa, addu'a kawai yaketa yiwa Zaleehan, dan dagani tanajin wahala, sosai yakejin tausayinta bare in ya tuno zancen likitoci, in kuma ya tuna mafarkin da yayi sai yaji sanyi kaɗan a ranshi.
Haka su Ummi sukayi jigum jigum dan gaba ɗaya acikin tashin hankali suke Ya Ahmad da ya

Ameenu ma da Aunty Lubna da Ziyada sun taho Zakariyya da Hayatuddeen kuwa suna can cikin gari.
Acan cikin labour room kuwa duk yanda Zaleeha ke tunanin ciwon na ƙuda ashe ya wuce tunaninta, sosai tasha wahala, gaba ɗaya jikinta ya jiƙe da gumi, addu'a take yi tare da ambaton sunan Allah.
Ta gigice sosai,
haka yasa cikin rauni tacewa ya Adnan da yake cikin doctors ɗin cewa dan Allah a kira mata Hamma Saif.
To al'barkacin Ya Adnan yasa aka barshi.
Yana shigowa ya matso gabanta cikin rawan murya dake baiyana tsantsar azabar da takeji tace.
"Hamma Saifuddeen zan mutu ka yafe min duk wani abinda nai maka na zahiri da baɗiri".
Da sauri ya ɗan sunkuyo kanta da nufin zai kissing goshinsa,
ɗai-dai lokacin kuwa yaro ya kawo kai nishi mai ƙarfi ya taho mata.
Ruggumeshi tayi gam a jikinta da ƙarfi ta saki nishe.
Cikin ƙarfin ikon Allah kuwa, ta kuma ƙara danna wani irin nishi hakanne yasa likitoti suka taimaka mata wajen zaro mata yaronta na miji, ajiyan zuciya ta sauke mai nauy,
shi kuwa Hamma Saif jin kukan jaririne da kabbarar da likitocin keyi yasashi.
Yin wani mashahurin murmushi tare da ƙoƙarin tasowa,
Ido ya zaro da ƙarfi jin wani irin ruggumeshi data kuma ruggumar da saida yaji numfashin shi zai ɗauke,
cikin sanyi murya can ƙasa yace.
"Wayyo ya Adnan ta shaƙeni".
ita kuwa Zaleeha nishi takeyi a jere a jere sabida kan yaro da ya sako kai.
wani yunƙurin tasakeyi sai kuma ga wani yaron ya sake faso kai, da sauri suka amshi ɗan.
Kabbararin da sukayi a wannan karon yafi na forko domin wannan alamace ta hasashen likitocin baiyi dai-dai ba.
A take aka yanke cibiyoyin yaran akazo da nufin za'a ɗaura mata su kan cikinta,
da sauri babban doctor ya hana tare da ce musu.ai da sauran wani a cikinta dan ga cikin yana motsawa,
tashin hankalin su kuwa yadda jini ya ɓalle mata,
madadin zafin naƙuda sai ta fara lumshe ido alamun bacci zatayi,
cikin tsoro Dr Sulaimi dake gefenta ta fara bubbuga kumatunta da ƙarfi alamun ta farka karta rufe ido.
Amman ina,
Dr Adnan kam sosai ya gigice.
Saifuddeen kuwa sai numfarfashi yake fidda jin ta sakeshi,
da sauri Babban Dr ya kalli Saifuddeen yace ya rinƙa kiranta.
A kiɗime Hamma Saif ya sunkuyo kanta tare da fara mgn da ɗan ƙarfi kamar yadda likitocin suka umarceshi.
"Zaleeha tashi buɗe idonki tashi kiga yaranmu, Zaleeha ki bude idonki".
A hankali ta fara buɗe idanun nata sabida, muryarshi da take jiyowa.
da sauri Ya Adnan yace.

"Kiyi nishi kiyi nishi da ƙarfi".
Ina bazata iyaba ga alamun Baby kuma ta sako kai,
dole Dr Sulaimi ne tazo tasa hannu da dabarun su na likitoci ta fara nemo kan yaron ita kuwa Zaleeha jin murya Hamma Saif na ce mata tayi nishine yasa ta ɗan rufe idonta, yunƙuri ta sakeyi da ƙarfi aiko da sauri suka sake zaro mata kyakkyawar ƴarta mace, amatuƙar wahalce take sakin ajiyar zuciya me ƙarfi,
cikin farinciki doctors ɗin suka kimtsa yaran sannan itama suka gyarata tsab, take suka mata alluran bacci dan tana buƙatar nutsuwa sosai.
Ganin tayi bacci yasa suka kwaso yaran suka fito dasu, rige rigen amsan yaran akayi tsakanin Ummi da kuma Mamy da Raliya dasu Ahmad, cike da matsanancin mamaki suke kallon kyawawan jariran yara uku reras Saifuddeen kuwa yama kasa magana sai kukan farin ciki da yakeyi yana ruggume da ƴarshi macen.
Ummi da Mamy kuwa suka amshi mazan masu matuƙar kyau,
cikin mamaki Ummi ta dubi nurse din, amamakance tace. "Nurse duka waƴannan kyawawan ƴaƴan yanzu Zaleeha ce ta haifesu." Kai nurse din ta jinjina alaman.
"Eh." Kabbara sukayi dukansu, yayinda Saifuddeen ya miƙawa Adda Rahma ya macen kana ya durƙusa yayiwa Allah sujjada, cikin matsanacin farinciki Ummi ta shafa fuskokin su, abayyane tace. "Alhamdulillah Allah abun godiya".
Saifuddeen ne ya bukaci daya ga Zaleehan sai-dai doctors ɗin basu bashi daman hakan ba, sunce ya bari saita farka ya Adnan kuwa daya fito dariya yayi taiwa Saifuddeen yana cewa.
"Baban yara kasha shaƙafa,
ai in mace na naƙuda kada ka yarda kana mijinta ta kiraka ka motso domin babu shakka zata shaƙeka".
Ahmad da Salisu da Mudassir da Warisu kam dariyar ƙeta suka saka.
Raihana kuwa da Iya da Baba Bellon suna harami.
Ya Ahmad ne ya matso jikin Mamy ya amshi yaron dake hannun nata,
Ya Ameenu kuwa ƴa macen ya amsa masha Allah.
Ahmad kuwa mijin Raliya ɗan dake hannun Ummin ya amsa.
Haka dai suka dinga kiran ƴan uwa suna faɗa musu, Baba Malam da Mama, ba ƙaramin farinciki sukayi ba dajin hakan.
Haka dai suka wuni a cikin asibitin, koda Zaleeha ta farka, sosai taji daɗi, saidai tasha mamakin ganin cewa wai itace ta haifi ƴan uku, sosai tayiwa Allah godiya,
Sai daren aka basu daman shiga inda take.
take kuwa suka shiga tarairayanta kaman ɗanyen kwai, ko awajen bawa yaran nono saida akasha fama da ita sosai saida taga Hamma Saif ɗinta ya ɓata rai sannan tace.
"To zan basu amman sai anjima".
Cikin fahimtar kunya takeji yasa gaba ɗaya suka fita.
Shi kuwa Saifuddeen a hankali ya matsota da kyau tare da cewa.
"Ki fara baya Mamana kinga itace karama kuma itace mace tanada rauni".
Cikin tura baki da alamun gaji tace.
"To bakaji iya tace ai wai sai an wonke bakin nonon".
Baki ya ɗan taɓe tare da cewa.
"Rabu da iya ita tana zaton ma'auranta yanzu irin na zamanin dane, da bata san nononmu fes

yake,
abinda kullum sai nasha abuna na more wani datti zaiyi? Ba datti ko kaɗan kuma dama nayiwa yarana tanadɗin nipples sun fito ras".
Ya ƙarishe mgnar yana ɗaura mata yarinyar a kan cinyarta.
a hankali yasa hannunshin cikin rigarta ya kamo nonon, a hankali tace.
"Wash Hamma Saif, in na basu suna shan bazanji komai bako?".
Dariya yayi tare da cewa.
"Ke tafi daga nan, waɗannan yaranki ne na cikinki ko sau dubu sabanin zasu tsotsi nononki bazakiji komai,
sai dai in nine na tsotsesu nanne kwaɗayinki zaisa kiji kinata yoyo ki jiƙe kiyi ta min ihu".
murmushi tayi tare da kauda kanta cikin jin kunya.
Sunkuyowa tayi ta kalli yaran a take taji sonsu na ratsata,
a hankali ta sunkuyo ta sawa macen nononta,
da sauri ta rufe idonta domin kamawa da ƴar tayi zafi taji,
shi kuwa Hamma Saif ɗaya yaron ya ajiye meta a gefen cinyarta tare da bashi nono ɗayan.
Da sauri ta kalleshi tare da cewa.
"Hamma Saif yaran ƙanana basuyi ƙatti ba".
Kanta ya shafa tare da cewa.
"Zasuyi ƙatti in sha Allah shiyasa nake son ki fara shayar dasu tun yanzu".
Kai ta gyaɗa kana cikin alamun yanayin raunin masu jego tace.
"Hamma Saif tun safe basuci komaiba ne?".
Kai ya jujjuya mata kana ya ɗauki ɗayan ya ruggumeshi tare da cewa.
"A a tun da safe na basu ruwan dabino sunsha sunyi nak sannan sunsha zam-zam shisa sukayi ta baccinsu".
Kai ta gyaɗa tana mai jin wani irin daɗi a hankali tace.
"Honey ita wannan dani take kama, shi kuma wannan da kai take kama, na hannun ka kuma to da waye yake kama".
Murmushi jin daɗi yayi tare da cewa.
"Shi wannan da Autan Ummi  yake kama wlh sak Hayatuddeen".
Da sauri tace.
Hayatuddeen yaga babies ɗinsu dan yasan kafin su dawo suma ɗin sun dawo.

Washegarin  kuma abokan  Saifuddeen suka nuna matsa zallan bajinta, inda kowannensu ya sayawa yaran kayayyaki masu kyau da tsada.
Haka rayuwarsu tayi musu dadi sosai, inda Zaleeha ta koma kamar da ɗinta, idan kaganta bazakace itace ta haihu ba, dan jikinta fresh, sannan cikinta ya zama flat, sai wani shinning take.
Ranan da yara suka cika kwana bakwai,  Saifuddeen  ya raɗawa kowannensu suna Babban shiyaci sunan Abba Muhammad kenan,  za'ana ƙiransa da sunan (Khareem)  sai me bimasa wanda aka sa masa Sunan Nurudeen, shikuma za'ana ƙiransa da  (Khasim)  itakuwa  baby girl sunan Ummi aka sa mata wato Fateema, inda za ana ƙiranta da (Khausar)   Ummi taji daɗin hakan sosai,  aranan kuwa wani irin gagarumin walima suka haɗa, Raguna uku da  suka yanka, haka suka kwaso masu aiki suka babbake musu naman, diner sukayi me rai da lafiya, inda

Zaleeha tasha kwalliya sosai kaman wata sarauniya, duk inda ta gilma, Idanun Saifuddeen na kanta,  daya kalleta kuwa zai kalli ƴarta Fateema wato Khausar, wanda take matsanancin kama da ita,  komai na Zaleeha yarinyar tana dashi, sauran maza biyun kuwa Dukansu da Saifuddeen suke kama kaman antsaga kara, saidai Khareem ne idan ka zuba masa idanu sosai zaka ga yana shige da Hayatuddeen,  hakanne yasa Hayatuddeen da Zakariyya bakinsu ƙin rufuwa, sosai sukeson yaran, hakan yasa kullum cikin ɗaukan hoto da yaran suke.                   Yau ya rage saura kwana uku su koma Nigeria,      Bayan sun gama dinner ne Raleeya ta kalli Hamman nata, cikin kulawa tace.
"Yauwa Hamma dan Allah inason roƙonka wani abu."
Murmushi yayi tare da cewa.
"Inajinki Raleeya ki roƙeni kome kikeso aduniya matuƙar ina dashi zan baki Insha Allah."
Idanunta ne suka ɗan kawo ƙwalla, cikin rau rau da ido murya na rawa tace.
"Dama ko Hamma Saifudddeen Aunty Zaleeha ce ta min al'khairi wai in ta haihu zata bani ɗan, to kuma gashi Allah yasa har uku muka samu,
Dan Allah Hamma kabani ɗaya daga cikin yarankan nan kaji, ka ga ni har yanzu Allah baibani haihuwa ba, kuma ina matuƙar son yaran".      Idanunsa ya zuba mata, take yaji wani irin matsanancin tausayin ƙanwar tasa ya rufesa, tasowa daga inda yake yayi, tare da ƙarasowa ya zauna akusa da ita, hannunta ya kamo cikin kulawa yace.
"Kin wuce haka awajena Raleeya, komai nawa nakune, komai na mallaka aduniya, naku ne, bazan taɓa iya hanaku abun da kikeso ba, ke ƙanwatace ta jini wanda nake matuƙar so, saidai kuma kiyi haƙuri bazan iya baki Khausar ba, saboda kinsan tundaga kanki ba a sake haifa mana mace a familyn mu ba, ganan Zaleeha itace mahaifiyar yaran, nasan bazata taɓa hanaki ɗanta ba, nasan zata amince saboda haka nabaki dama daga kan Adeel, Kareem, Kasim, ki zaɓi duk wanda kikeso acikinsu na bakishi halak malak."      Wani irin matsanancin farinciki ne ya rufe gaba ɗaya zuciyoyinsu, hakan yasa Raleeya ta faɗa jikinsa ta rungumesa.  Murmushi Zaleeha tayi, tare da cewa.
"Ƙwarai kuwa Raleeya ƴaƴanmu ƴaƴanki ne, saboda haka ni bancire Khausar aciki ba, duk wanda kikeso acikinsu ki ɗauka kawai mun baki kyauta."
   Cikin jin daɗi Ummi taɗan goge hawayen daya taru agefen idanunta, tabbas tana sake godewa Allah daya kawo mata farinciki acikin zuri'arta.
Ahmad dake murmushi Raleeya ta kalla, cikin farinciki tace.
"Ya Ahmad wanne zamu zaɓa daga ciki?".   Cikin jin daɗi yace.
"Kowanne kika zaɓa nima shine zaɓina, mungode da karamci ƙwarai Hamma Saif Allah yasa next year a haifo mana ƴan 6".
   Dariya suka sa dukansu.
Nan Raleeya tace ta ɗauki Kareem  dan yaron ya kwanta mata arai ƙwarai, daɗin daɗawa kuma gashi bashi da hayani ya, ga kuma ɗiban kama da sukeyi dana hannun damanta wato Hayatuddeen gashi kuma shine mai sunan Abbansu.
Hayatuddeen kuwa baki ya tura tare da cewa.
"Kuma shine a rasa wanda za'a kyautar sai mai Kanada Ni".
Dariya Raliya tayi tare da cewa.
"Yaro danma ina sonka ne na zaɓi mai kama da kai".
Aifa nan sukayi ta dariya da hirarsu ta yan uwantaka ganin haka itama Zaleehan ta zame ta tafi

wurinsu Ziyada da Ya Ameenu da Aunty Lubna da Ya Ahmad da ya Habu da Zakariyya tana shiga Zakariyya ya amshi Kausar tare da cewa.
"Allah ko ya Ahmad ina kama da Kausar ko?".
Ziyada ce tai ɗan murmushi tare da cewa.
"To ai kana da kamanni da Adda Zaleeha shisa kakega kuna ɗan kama da Kausar".
Kai Ya Ahmad ya jinjina tare da cewa.
"Hakane kuwa".
Nan ya Ahmad ya kira musu Baba Malam video call, sosai sukayi ta hira,
sai Saifudddeen ya kira Zaleeha kafin ta koma can inda suke sukaci gaba da hira.

Haka dai suka sha hiransu awannan rana, koda dare yayi bayan Zaleeha ta shayar da Kareem miƙawa Mamansa Raleeya tayi, tare da cewa.
"Gashi kuje kuyi hira in yayi kuka a kawoshi yasha nono".
ai kuwa cikin zumuɗi Raleeya ta amshesa tawuce ɗaki, Ahmad ne ya rufa mata baya, haka suka saka yaron atsakiyarsu, suna rungume da juna ahaka sukayi ta hira.
Dama ko ɗar Ahmad bai taɓa damuwa da rashin haihuwan Raleeya ba, duk da tsananin son haihuwar da yake musamman ƴa mace amman baya sa damuwa a ransa saboda yasan da haihuwa da rashinta duk na Allah ne, kuma komai nada lokaci, watarana suma Insha Allah zasuga ƙwansu aduniya.

Haka dai sukayi rayuwarsu ta saudiya cikin jin dadi, wayewar garin yaune jirginsu zai tashi.

Hakan yasa tun wuri suka kammala kintsa komansu, ƙarfe takwas ɗin safe kuwa dai-dai jirginsu ya ɗaga zuwa Nigeria.

Koda suka sauƙa a Nigeria kuwa, dukansu suka ɗunguma zuwa gidan Ummi, su ya Ameenu kuwa suka nufi gidan Baba malam .

Anan suka samu Ameena ta baje basiranta wajen yi musu girke girke kala kala, inda Laure mai aiki ta taya ta da wasu abubuwan.

Suna isa kuwa ba abun da Ameena ta fara buƙatar gani kaman kyawawan yaran Zaleehan cikin matsanancin farinciki ta ɗaukesu tana musu kallonshi Kasim sak Adeel ɗinta.
Adeel kuwa da ɗan gudunsa yazo ya rungume Zaleeha cikin gwarancinsa yake cewa.
"Owowo ohon Ammi". dan ko takan Babansa be biba, Amminsa kawai ya kula, haka yasa Zaleeha ta ɗagashi sama tana yi masa wasa cike da soyayyarsa.

*LITTAFINA NA KUƊINE idan kina buƙatar saya turo katin mtn na ɗari uku ta wannan layin 09097853276 ko kimin transfer 300 ta asusuna na 0005388578 jaiz back Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo min shaidar biyarki ta wannan layin 09097853276 biya ɗarinki uku kacal da ki karanta ba tare da haƙƙin kowa a kankiba*

Ban samu damar yin editing ba...!

By

Murmushi sukayi dukansu, cikin kulawa da farin cikin ganin babban ɗan nashi Saifuddeen yace.
"Lallaima Adeel wato Amminsa kaɗai ya sani, ni ko kewata ma baiyi ba, bare ma har yazo yaɗan rungume ni, yamin irin oyoyo Dad dinnan". Dariya Zaleeha tayi tare da cewa.
"Ai kaima sai haƙuri Hamma Saif kasani, kuma kowa yasan Adeel nawa ne na hannun dama nane, saboda haka ni zai fara yiwa oyoyo kafun kowa, ko ba haka ba mangana my sweet and lovely father". Cikin gwarancin magananansa wanda da wuya ake ganewa yajin jina kai tare da cewa.
"Ammina kin shayomin tsayaba ko?".
Murmushi tayi tare da ɗan shafa kansa, cikin ƙaunarsa tace.
"Sosaima kuwa sweetheart ɗina, nasayo ma tsaraba me yawa, dan naka tsaraban ma yafi na kowa yawa, nasan zakaci chocolate ɗin saudiya ko, to maza buɗe baki sai na baka chocolate me daɗi."
Ɗan ƙaramin bakinsa me kama dana babansa ya wangale,
chocolate ta ciro daga jakanta tare da ɓarewa ta saka masa abaki.
Ɗan tauna chocolate ɗin yayi, tare da lumshe idanunsa, cikin gwarancin magananansa yace.
"Ummm Ammi choco dadi."
Murmushi Zaleehan tayi tare da sake jawosa jikinta ta rungumesa, su dai su Ummi murmushi kawai sukeyi, dan soyayyar dake tsakanin Zaleeha da Adeel sai Allah.
Anan cikin falon Ummin suka zauna, Ameena kuwa tana ruggume dasu Khareem sai yaba zallan kyau da kuma kwarjinin yaran take, haka ta rungume Khausar ajikinta, tanajin kaman ta maida yarinyar cikinta, sosai yarinyar tayi mata kyau sumbatar goshinsu taitayi ɗaya bayan ɗaya. Cikin kula da son ƴarinyar ta kalli Zaleeha da Saifudddeen tace.
"Ni dai ga tawa, duk na bar muku mazan amman wannan tawace".
Murmushi Zaleeha tayi tare da cewa.
"Abu naki mgnin a kwaɓeki, Ummu Khausar tunda abin son kaine har an wani waremu".
Dariya su Ummi sakuyi,
Hayatuddeen kuwa tura baki yayi tare da cewa.
"Nida naso Khareem sai aka hanani Raliya da azarbaɓi ta rigani gashi yaro dani yake kama an wani bawa shi su Raliya".
Cikin dariya Ameena tace.
"To wa zai bawa tuzuru ɗan shi".
Da sauri ya haɗe fuska tare da cewa.
"To kuma ce miki akayi tabbata zanyi bazanyi aureba ne, kadama ku bayar ai ba sai na roƙeku bama ɗauka kawai zanyi".

Dariya sukayi dukansu.    Haka dai sukayi ta hira da dariya.
Bayan kuma sun nutsune suka ci abincin da Ameena ta dafa musu mai rai da lafiya,   tun kafun ma sugama kammala cin abincin   Zaleeha kejin wani irin bacci, zaman cikin jirgi duk yasa jikinta yayi laushi,
hakanne ma yasa koda suka kammala cin abincin  ita tafara tashi daga kan dinning table ɗin, sallama tayiwa su Ummi sannan   tawuce sashinta, bayan tabar Khasim awajen Ummi, Khausar kuwa na gun Goggo Dada, Khareem kuwa dama na Raleeya ne, hakanne yasa Hayatuddeen ya riƙesa yana ta masa wasa, da yake yaran basu da wani yawan hayaniya sosai, hakan yasa tun ɗazu baccinsu suke ta sha cikin kwanciyar hankali, koda taje ɗakin nata, wanka tayi sannan ta kimtsa kanta cikin wasu kaya marassa nauyi, akan gado tayi kwanciyarta, tana sauƙe numfashi.

Acan sashin Ummi kuwa, Saifuddeen  zama yayi afalon suka sha hira da Umminsa,  da kuma su Goggo Dada, ananne ma Ummi ke sanar masa cewa, gobe ya tura Sule driver Mala inna  ya ɗauko Inna Shatu, wato gwaggon Ummin kenan wacce take gidan Baffan Ummin,  kasancewar itace zata kula da Zaleeha, wajen yi mata wankan jego me kyau, za kuma ta gasata yanda ya kamata.
Sosai Saifuddeen ɗin yayi na'am da ɗauko Inna Shatu'n, dan shima ya fiso Zaleehan ta samu jego me kyau, sannan kuma agasa masa ita yadda ya kamata, tayanda ranan da ta gama arba'in zai kwashi ganima.

Bayan sun ɗan taɓa hira da Ummi ne, ya kwashi ƴaƴan nasa, saida safe yayiwa su Ummi, sannan ya nufi side ɗin Zaleehan dasu.
Yana tafiya su Ummi ma kowa ya tafi ɗaki, dan suma suna so suɗan huta.
 Hayatuddeen kam dama ya jima da shigewa ɗaki, Ahmad da Raleeya ma suntafi ɗakinsu na da, duk kuwa uban gajiyan da suka kwasowa kansu, Ahmad bai bar Raleeya ba, saida ya tsotseta son ransa, haka suka biyewa juna, inda suka ƙarawa kansu gajiya akan wanda suke dashi, fatansu suma akullum shine, Allah Ya basu nasu rabon me al'barka, dan koda sukaje Umra ma addu'an da sukayi tayi kenan, dan bazasu fidda rai da raboba, komai ikon Allah ne.

Saifuddeen kuwa koda yaje ɗakin Zaleeha, kwance ya sameta tana baccinta cikin nutsuwa, jikinta kuwa sai tashin fitinannen ƙamshi yake, har yanzu tana nan a Zaleehanta, ƴar ƙwalisa, me kyau da diri, babu wani abu daya sauya mata, dan bama zakace ita ta haifo yara har uku reras ba,   kan wani haɗaɗɗen ɗan madaidaicin gado ya shumfuɗe yaran, saida yayi kissing ɗinsu dukansu, kafun ya sakarwa mamansu itama wani zazzafan kiss, cike da kewarta yaɗan shafa  fuskarta, cikin ƙasa da murya yace.
"I love you my   babe,  have a sweet dreams."        Kashe musu wutan ɗakin yayi sannan ga fita.

Kaitsaye part ɗin Ameena ya nufa, koda yaje ya samu ta gama kimtsa kanta cikin kayan bacci masu kyau, sai ƙamshi takeyi zubawa, tayi parking  gashinta atsakiyar kanta.  Hannayensa ya ware mata,  anutse kuwa tazo ta shige jikinsa,    kissing ɗinta yayi, sannan yaja hannunta suka fita zuwa bedroom ɗinsa.
Suna shiga kuwa yasa ta haɗa masa ruwan wanka, kayan jikinsa ya cire sannan ya kama

hannunta suka shige toilet ɗin tare,  ita ta taimaka masa yayi wanka, saidai tun kafun ya gama wankan ya lallatseta son ransa,  suna fitowa daga toilet ɗin kuwa  yajata sukayi kan bed, romancing ɗin juna sukayi sosai, kafun daga bisani suka faɗa duniyar ma'aurata,  kasancewar rabonsa da sex tun kafun Zaleeha ta haihu, baya taɓa manta wata rana da yayi sex da ita, wanda dagananne kuma bai kuma ba haihuwa yazo mata, aranan yaji wani abu waishi dadi, yayi sambatu har kaman laɓɓan bakinsa zasuyi ciwo,
hakanne yasa yau daya ritsa  Ameena yayi mata kekkyawa kamu da wutar bege da kewa, ya jikkata sosai, dan har wani zafi zafi takeji aƙasanta, dan ta gurzu baɗan kaɗan ba.
Atare sukayi wanka, sannan suka kwanta maƙale da juna.

Washegari kuwa,  bayan sun kammala break fast, su Baba Malam, da Mama  suka samu isowa, dan duba me jego da kuma yaranta, kaya sosai suka kawo mata masu yawa, haka Mama  tayi rawar gani sosai.
Baƙaramin daɗi kuwa Mama taji aranta ba, musamman ganin yanda Zaleehan ta ta sake zama babbar mace, gashi kuma ta haɗu da surukai na ƙwarai.

Su Baba Malam basu tafi ba, Ziyada da Ya Ameenu suka zo.
 farinciki awajen Zaleeha ba'a magana,   dan taji daɗin ganin yadda Ziyada ta meye mata gurbin Adda Maryam, koda suka gaisa da mamaki tace.
"Ziyada har gajiyan hanyar ya wuce ne?".
Murmushi tayi tare da cewa.
"Wlh akwai gajiya kam Adda Zaleeha kawai dai a kwana ɗayan nanne da banga su Khausar bane naji inata kewarsu, shine nace ya Ameenu ya kawoni mu gansu, yace min to dan dama wai bai bada kayansu ba". Sosai Zaleeha taji daɗin ganin
 ƙanwarta ta sosai, babban abun farincikin ma shine yanda taga Ya Ameenu ya fara dawowa da fara'arsa, gashi yayi wani irin fresh yayi kyau wanda ita batama lura da hakanba a Saudiyya sai yanzu, dagani kasan yana samun kulawa  awajen Ziyada, itama dai Ziyadan hakanne dan  tayi fresh, ta kuma ƙara girma daganinta kasan akwai shigan ƙaramin ciki ajikinta, saboda tumbinta daya ɗan  tasa, sai ɓoyesa  take acikin mayafinta, batason agani, wai kunya takeji.

Zuwan su Ya Ameenu ne yasa su Baba Malam suka ɗan jima agidan,   lokacin da Saifuddeen yazo suka gaisa, Mama tasha mamaki da ta gansa, domin miƙewan ƙafafuwan nasa yasa ya ƙara zama wani hamshaƙin Namiji,   babban abun dayake sata jin kunyansa kuwa, shine yanda yake matuƙar girmama ta, duk da yasan cewa ada batason aurensa da Zaleeha, amma hakan baisa yaƙi bata girmanta ba, sosai yake girmamata, amatsayinta na Mamar matarsa, dan  har saima ya rusuna  ƙasa yake iya gaisheta.    Hira suka ɗanyi kaɗan, kafun suka soma ƙoƙarin tafiya.
Kusan ma atare Ya Ameenu dasu Baba Malam din suka tafi, shima Ya Ameenu'n akwati guda ya cikawa Zaleeha da kayan babies da kuma nata itama, Ziyada ma tayiwa babies din kaya masu kyau, koda suka keɓe da Zaleeha, wasu magungunan mata masu kyaun gaske ta bawa Ziyadan, tare da faɗa mata yanda zatayi amafani dasu, dan itama  a saudiya ta sayo su, magunguna ne masu kyau da inganci, batabar Ziyadan haka ba, saida ta haɗata da kayan ciye ciye, sannan ta bata wasu irin fitinannun sexy wears masu kyau wanda tasayo daga can

Instanbull, sosai Ziyada taji daɗin kyautan, dan ayanzu tana matuƙar son Ya Ameenu'n nata, domin kuwa bakaɗan ba yake shayar da ita madaran soyayyarsa, tana matuƙar son irin wasannin da yake mata, hakanne kuwa yasa shaƙuwa me ƙarfi ta shiga tsakaninta dashi, yana tarairayanta yanda ya kamata, hakanne yasa itama ta sakar masa jikinta sosai.
Har bakin mota Zaleeha da Saifuddeen suka rakasu, saida sukaga tafiyarsu sannan suka koma cikin gida, zuwa lokacin kuwa tuni Saifuddeen yasa Sule driver ya tafi ɗauko Inna Shatu a Mala,inna, falon Ummi suka koma suka sha hiransu, Ahmad na ganin ƙarfe 11 tayi yace wa Raleeya tazo su koma gidansu,  Dariya sosai su Ummi sukayi, dan sunsan Ahmad yafaɗi hakanne dan bayason Raleeyan tayi musu lunch,  haka kuwa sunaji suna gani, Ahmad ya tasa Raleeya agaba suka tafi, sai dariyan mugunta yake yana ce musu.
"Wai shi matarsa ta gama bauta."
Koda Ummi tace su tsaya suyi lunch, tunda Laure me aiki ta ɗaura abincin, cewa yayi
"A a mun gode da tayi Ummi zamu biya restaurant muci."
Haka dai suka rabu sunata wasa da dariya.

Bayan anyi sallan azahar ne Sule driver ya dawo daga mala'innq, shida Inna Shatu, tarba me kyau Ummi tayiwa Inna Shatu'n,  bayan sun ɗan gaisa taci abinci ne, Ummi tace Zaleeha ta kai Inna Shatun masauƙinta,  inda anan cikin sashin Zaleehan masauƙin Inna Shatun yake a ɗaya bedroom ɗinta ta sauketa.
Hakan kuwa akayi, har ɗaki Zaleeha takai Inna Shatu sannan tace mata taɗan ƙara hutawa,    ai kuwa bayan Inna Shatu ta huta aranan  ko kwana ba ayi ba,  ta saka Zaleeha agaba,  tayi fara bata dukkan cikekken kulawa irin na masu jego da jogo mai rai da lafiya, sosai ta gasa mata jikinta, bayan tayi wankan kuwa tasa ta tayi tsuguno da wani shu'umin turare me ƙamshin gaske, sannan ta bata abinci irin na masu jego taci.

Bayan anyi sallan isha ne Saifuddeen  ya shigo cikin ɗakin, ganin haka yasa Inna Shatu basu waje, suka sha hiransu,  sosai Saifuddeen yake begen  Zaleeha, dan ƙamshin da take na neman hautsuna tunaninsa,   da ƙyar  ya iya controlling kansa, saida safe ya mata, bayan yayi kissing ɗinta, sannan ya nufi sashin sa, acan ya samu Ameena na jiransa, ai ba wani jinkiri ya fara romancing ɗinta, dan abuƙace yake sosai, saida ya samu nutsuwa sannan suka kwanta sukayi bacci yana sa mata al'barka a zahiri a ransa kuwa cewa yake.
"Lallai kam mai mata ɗaya aminin Gwaurone".

Washegari.
Da sassafe Inna Shatu ta kuma yiwa Zaleeha wankan tafashashshen ruwan zafi, tare da haɗa mata tea me kauri tasha,  bayan tasha tea ɗinne kuma ta bata abinci, irin wanda ya kamata ace me jego taci,  ai  kuwa Zaleeha bata ƙi ba taci abincin sosai, dan cima ne me kyaun gaske.
Inna Shatun ne  tayiwa yara wanka ta shiryasu tsab cikin kayansu iri ɗaya masu kyau.

Asafiyan ranan ne kuma da misalin ƙarfe 10 Ya Ahmad da Aunty Lubna da Zahira sukazo da Zahiran wacce Zaleeha ta roƙa  a turo mata ita dan ta tayata kulada yara duk da ga Inna Shatu tana ƙoƙarin.
Su kuwa su Ya Ahmad sunzo su sallamarta ne dan gobe zasu koma Abuja.

Sosai Zaleeha taji daɗin zuwansu, tarba me kyau Ummi tayi musu, anan falon Zaleehan suka zauna, bayan sunje sun gaishe da Ummi, sam Ya Ahmad ya kasa ɓoye farincikinsa, sosai yaji daɗin ganin yadda ƴar uwartasa, take rayuwa da kishiyarta zama na amana da tsabtataccen kishi, ga ƴan kyawawa yaransu haka ya rungumesu aƙirjinsa yana ta musu wasa, saida suka kwashe awa ɗaya cas agidan Zaleehan kafun suka soma yunƙurin tafiya, har bakin mota Zaleeha da Saifuddeen da Ameena suka rakasu, Ananne suka buɗe bayan motar suka fiffito da kayayyakin da suka sayawa yaran, harma da Adeel, kayane masu uban yawa, saikace wanda za a bude ɗan ƙaramin kanti.
Saifuddeen da kansa yace.
"Gaskiya Ya Ahmad kayan nan sunyi yawa". murmushi kawai ya Ahmad din yayi tare da girgiza kansa, cikin kulawa yace.
"Ba wani yawan da sukayi, halan ko kun manta cewa nima ƴaƴana ne, saboda haka kome nayi musu ba zance yawa aciki, kasanima acikinsu ko akwai surukina ko surukata".
Dariya dukansu sukayi, tare da yi musu godiya sosai, saida suka ga tashin motarsu sannan suka koma cikin gida, anan falon Ummi suka zuba kayan suna nunawa Ummi, sai faman sanya al'barka take da kuma godiya, dan kowa yaga kayan yasan ankashe dukiya wajen sayansu.

Su kuwa su Ya Ahmad daga gidan Zaleehan direct gidan Ziyada suka wuce.
Dai-dai lokacin kuwa Ziyada na jikin Yaya Ameenu, yana bata tea abaki ya maida ita saikace yarinya ƴar shekara huɗu, duk ta sakalce masa, shiɗinma kuma biye mata yake, saboda ko bakomai itaɗin yarinya ce me biyayya agaresa, uwa uba kuma tana bashi gamsuwa sosai ta fannin auratayya ga larurar cikin da yake sata ƙin cin abinci, gashi kuma ta kasance jinin Maryam ɗinsa ne, kasancewar awajensa ko akuyace ta haɗa alaƙa da Maryam to tabbas zaiyi iya ƙoƙarinsa wajen bata kyakkyawan kulawa.
Jin sallaman su Ya Ahmad ne yasa tayi saurin sauƙa daga jikinsa, hijab ɗinta dake gefe ta ɗauka tasa, saboda wai ita kunya takeji aganta da ciki, dan tasan kowa idan ya ganta yasan me akayi da ita ta samu cikin.

Ita dakanta ta buɗe musu ƙofa suka shigo, da ɗan sassarfa ta haɗa Ya Ahmad da kuma Aunty Lubna ta rungumesu, cike da farincikin ganinsu tace. "Oyoyo Ya Ahmad da Aunty".
murmushi Ya Ahmad yayi tare daɗan shafa kanta, cikin kulawa yace. "Oyoyo my little sis".
Murmushi tayi tare da sakinsu, suka ƙaraso cikin falon, cikin farin ciki Ya Ameenu ya tarbesu, take Ziyada ta tafi ta kawo musu ruwa, bayan sun sha ruwanne suka sake gaisawa.
Nan suka ɗan taɓa hira, kafun Aunty Lubna ta jata zuwa ɗaki, anan falo suka bar su Ya Ahmad da Ameenu suna tattaunawa, acan ɗaki kuwa wasu magungunan mata masu kyau Aunty Lubna ta bawa Ziyada, tare dayi mata bayanin yanda zatayi amfani dasu, sannan kuma tace mata kada ta yawaita shansu, ta bisu ahankali, ba aso kana sha da yawa, musamman ma ita da take da ƙaramin ciki, tace dazaran kuma sun ƙare tayi mata magana, zata aiko mata da wasu haɗin masu kyau.
Akunyace Ziyada tayiwa Aunty Lubnan godiya, dan wanda Zaleeha ma ta bata tasha ta kuma ga amfaninsu, dan aranan Ya Ameenu saida sambatunsa ya ninka na kowanni rana, duk dama tuncan idan yana sex da ita yana nuna mata jin dadinsa afili, dan haka zatajisa yana ta sakin

gurnani, tun tanajin nauyinsa har ta riga da ta saba.
Hira suka ɗanyi da Aunty Lubnan acikin ɗaki, kafun suka fito falo.
Suna fitowa kuwa Ya Ahmad yace da Lubna su wuce, hakan kuwa akayi, har bakin mota suka rakasu, da ma sukazo tafiyane Ya Ahmad ya ja Ziyadan gefe yaɗan mata nasiha, kyautan kuɗi ya bata 100k, inda yace mata.
"Tana amfani dashi idan wani buƙata nata ya tashi, bayason tana yawan tambayan Mijinta kuɗi, duk dama Ya Ameenu'n matsayin Yaya yake awajenta, amma dai yawan bani bani ga miji ba daɗi musamman ita da bata da aiki bata kuma sana'a"
Ƙin karɓan kuɗin tayi, ɓata fuska Ya Ahmad yayi, tare da sawa ta karɓa dole, godiya tayi masa sosai sannan sukayi sallama da yi musu fatan Allah ya maidasu lfy.

Acan gidan su Saifuddeen kuwa bayan kwana takwas da dawowansu, su Ishaq ma suka dawo daga India, ansamu nasara sosai kuwa a aikin da akayiwa Ishaq, dan yanzun dishi dishin da yake gani ma ya washe, saidai ace Alhamdulillah.

Ranan da suka sauƙa agidan su Saifuddeen ganin Babies, sosai kowa yaji dadin ganin yanda Idanun Ishaq ɗin suka buɗe, yana ganin kowa kamar yanda kowa ke ganinsa, bakaɗan ba Ummi taji dadin hakan, take kuwa ta haɗa musu ƴar walima me ƙayatarwa shida abokansu duka, Ishaq kuwa yaji dadin hakan sosai, tabbas Ummi Uwace ta gari, da nata da wanda ba nata ba duk ɗayane awajenta, bata nuna banbanci.

Ranar wata asabar ne Zaleeha takewa Saifudddeen batun itafa bazata amsheshi daga gama arba'inba sai yaranta sunyi wata uku kafin nan sunyi gwaɓi sun girma.
Ai fa nan ya haɗe fuska yace.
"A a shekara uku dai ba wata uku ba, kice kin gaji dani kawai mana".
Cikin mmki tace.
"A a daga kawai nace wata uku sai ka haɗa fuska, ni bance na gaji da kaiba Hamma Saif".
Fuskarshi ya kuma haɗawa tare da cewa.
"Bana so kar in sake jin mgnar nan a bakinki kada ki bari ranki ya sake raya miki hakan bana sam, kina gama arba'in zaki amshi girkin".
Shiru tayi ganin yadda ya haɗe fuska da alamun ranshi ya ɓaci.
Shi kuwa miƙewa yayi ya kontar da Khausar dake hannunshi kefen Khareem da Khasim a hankali ya juya ya nufi hanyar fita har yaje bakin ƙofa sai ya kuma ɗan juyo ya dawo gabanta, key ɗin sabuwar mota ya miƙa mata, kana yace.
"Ga key ɗin ki, bari inje in bawa Ummu Adeel ma tata, in mutu a kanku ku ganina ma bakwa son yi".
Da sauri ta ruggumeshi tare da manna mishi kiss a goshi cikin jin daɗi tace.
"Mun gode Abban Adeel Allah ya ƙara wadata ya rufa maka asiri duniya da lahira, muna sonka Hamma Saif in bamu sokaba wa zamu so, kayi haƙuri ni ko yau kace in amshi girki dole inbi umarni ka".
Bakinshi ya ɗan tura mata kana ya janye jikinshi ya juya ya fita yana murmushi tare da cewa.
"Amin Amin".

Ɗakin Ameena ya nufa, yana mai ƙara haɗe fuska dan itama ɗazu ta ɓata mishi rai dan ya nuna yanada buƙatar ta, tace mishi wai ya bari sai dare, ta shareshi tanata hidima da Khausar, kota kanshi bata biba.

Yana shiga, ya sameta gaban mirror tana shafa turare key ɗin ya ajiye mata a gabanta tare da cewa.
"Gashi motocin naku sun iso".
Da sauri ta miƙe sai kuma ta faɗa jikinshi cikin yanayin ban haƙuri da godiya tai ta kissing nashi tako ina tare da cewa.
"Na tuba kayi haƙuri, ka dena fushin nan, gani kayi duk yadda kakeso dani,
Allah ko ɗazuma bakaga Khusar ne taketa kuka Amminsu kuma ta shiga wonka".
Tureta ya ɗanyi tare da cewa.
"Ku ƙyaleni inyi duk yadda nakeso, ai na lura yanzu ba sona kukeba, yadda Zaleeha tai tamin lokacin Adeel na ƙarami haka kema kike min yanzu da an taɓaki kice Khausar, an dena son babanta da kula dashi".
Dariya tayi ganin yadda yayi mgnar a fili zaka gane irin yadda yake masifar son Khausar dan ko sunanta aka kira sai yayi murmushi son Khausar na da banne a zuciyarshi yana masifar son ƴarinyar tamkar ranshi, wani lokacin Ummina zai kirata wani lokaci kuma yace Zahra wani lokacin kuma yace Khausar ɗin,
jawoshi tayi suka faɗa bisa gado daga nan fushin ya tafi.

Alhamdulillah rayuwa tana tafiya a dai-dai, komai yana wakana cikin tsari da Hukuncin Allah.
Yau  sati biyar kenan da Haihuwan Zaleeha, kyakkyawan kulawa kuwa tana samunta daga wajen Inna Shatu da kuma Ummi,  uwa uba Hamma Saif dinta, sosai yake tattalinta da riritata, kullum dare sai ya tayata hira kafun yake wucewa zuwa ɗakinsa, inda dayaje kuwa zai gurji Ameena son ranshi, itama dai yanzu Ameenan wani sabon jaraba takeji dashi, dan kwata kwata kwana biyun nan  bata gajiya dashi, da zaran sun gama sex ɗin kuwa, zata soma yunƙurin amai, haka zataji ta mugun galabaita, har sai tasha yoghurt sannan take dawowa normal, koda tayiwa kanta pregnancy taste, result ɗinta ya bayyana cewa tana da ɗan ƙaramin ciki amma, bai wuce 3 weeks ba, saboda haka baiyi ƙwari ba,  tayi farinciki sosai, koda ta faɗawa Saifuddeen shima yayi farinciki, inda ya keta godewa Allah da irin ni'imar da yayi masa.

Ɓangaren Zaleeha kuwa jegonta take sha me kyau, cima masu ƙara lafiya take ci da sha, tayi wani irin haske da kyau, kullum idan ka ganta zakace a ingine ake sata awanke, komai nata yazama abun ɗaukar hankali.

Ɓangaren Hayatuddeen dasu Zakariyya kuwa karatu suke babu wasa, dukansu sun maida hankalinsu akan karatunsu, Khamis ma ya dage sosai,   yanzu sam babu ruwansu da wani kule kulen mata, waya ma basu wani damu da ita ba, saidai idan ya kama dole,  har yanzu kuwa Hayatuddeen najin Zahrah acikin ransa, idan ya kwanta har mafarkinta yake,  baisan meyasa ba, yana matuƙar son  Zahrah, ko tunaninta yayi sai yaji wani shauƙi aransa, duk  ran jumma'a kuwa sai yaje gidan Baba Bello wai ko zai ganta, amma sau ɗaya ya taɓa gamdakatar din samunta, shikuwa bayason fara zuwa gidansu daga yanzu, so yake sai ya faɗawa Hammansa

ya amince, sannan kuma sai karatunsa ya sakeyin zurfi,  kafunnan yasan yana da full confidence ɗinsa.

Akwana atashi asaran me rai, kwanci tashi ba wuya, yau dai gashi Watan Zaleeha ɗaya da kwana tara da haihuwa, inda gobene zata cika kwananta arba'in da Haihuwa kenan.   Sosai Saifuddeen ke jin dadi yana marari, har wani rawan ƙafa yake, dan amatuƙar ɓuƙace yake da ita, yayi masifar yin kewarta, musamman ma rafin daɗin ta, jiyake kaman sabuwar amarya za'a kawo masa.

Daga ɓangaren Zaleeha ma hakanne dan ta yi kewar mijin nata sosai, ga kuma wasu irin mahaukatan tsumi da ake bata tana sha, gyara Inna Shatu da Mama keyi mata bana wasa ba, kusan kullum sai tayi turaren tsugono, har takai ga ko fitsari tayi sai taji tashin ƙamshi na fita ajikinta, wani irin gyara suka mata naban mamaki, ita kanta jin cikin jikinta takeyi acike kaman budurwa, ga shi hips dinta sun ƙara girma, breast ɗinta kuwa dama sunanan atsaye tamtsan-tamtsan  wanda  kuwa take zaton bazasu kwanta ba, dan zata iya cewa gadon kyaun jiki tayi awajen Mamanta, dan Mama ma akwai diri.

Ita kanta ayanzu abuƙace take da Saifuddeen ɗin, musamman ma idan ta tuna abun daya wakana atsakaninsu daren jiya, sosai ya luguiguita ta tare da lasheta har saida ta fidda ruwa, akullum haka yake mata sai ya gigita mata tunani sannan yake barin ɗakin, wani lokaci ma har cewa yake, zaiyi sucking ɗinta, idan taƙi shine yake fingering ɗinta.

Ɓangaren Yaranta kuwa masha Allah, sun ƙara girma sunyi kuɓul-kuɓul dasu, idan ka gansu zakayi zaton ƴan wata biyu ne, sun ƙara kyau da shiga rai,  haka ma Khausar itama tana da yawan fara'a, kamanta da Mamanta kuwa yasake bayyana, dan harma tana ƙoƙarin fin maman nata kyau,  yarinyace me shiga rai, kullum kuma cikin kwalliya yaran suke, sai-dai ace Masha Allah, wani irin zazzafan soyayya Saifuddeen ke nuna musu, ko kuka yaji sunayi saiya tashi hankalinsa, yanason yaran sosai da sosai, wanda tsananin soyayyar da yakewa Zaleeha ne kuma ta shafesu yakan ɗaukosu da Adeel duka ya kawosu ɗakinshi ya ajiyesu gabanshi Adeel yayi ta gwari-gwarinshi yana taɓa yaran hakan yana masifar sashi jin daɗi tuni kuma yasa Ameena ta yaye mishi Adeel ɗinshi.

Ameena kam awannan karon tasamu Saifuddeen yanda takeso, dan yana iya ƙoƙari wajen sauƙe mata haƙƙinta mu samman daya gano masifeffen jaraban da cikin yasata gata dama gwana, bare kuma ga cikin, shi kam hakan yasa yake wadaƙanshi son ranshi, yau ma dai saida suka darji juna kafun ya tafi wajen aiki, ita kam batasan me yasa wannan cikin nata yazo mata da jaraba ba, dan bataƙi akullum Saifuddeen yayi sau uku ba, gashi cikin nata ba wani babba bane yanzune ma ya cika wata ɗaya, yanzu haka tunanin yanda zata iya kwana biyu batare da tajisa ajikinta ba take.

Saifuddeen kuwa ko awajen aiki kasa haƙuri yayi, saida ya ɗauki wayarsa ya ƙira Zaleeha, danji yake kaman shekara arba'in yayi baijisa acikin rafin daɗinta ba, duk da kasancewar Ameena ma tana da nata ni'iman, amman yana masifar begen matarshi.

Zaleeha kuwa gane cewa abuƙace yake, yasa tayi masa ƙasa da murya, take ta shiga wargaza masa lissafinsa da zafafan kalamai masu ɗaga hankali, haka ya biye mata ta jefasa cikin wata duniya ta daban, haka ya ƙarisa aiki adaddafe,  koda ya dawo gida, ya samu ta kulle ɗakinta ta ciki, yasan dagangan tayi masa hakan, kwafa yayi tare da cewa.
"Hmmm yarinya gobe idan na kamaki zaki faɗawa mutanen garinku."
ɗakin Ameena ya wuce, itama abuƙace ya sameta, hakanne yasa bawani wasa suka ɗaura daga inda suka tsaya, Ameena har kukan daɗi tayi, saboda tasamu abun da takeso.

Washegari Zaleeha ta cika kwananta arba'in da haihuwa, aranan ne kuma ta gama wankan jegonta,  wanda idan taso aranan zata amshi mijinta, idan kuma tana da ra'ayi zata iya bari sai zuwa gobe.
Saidai kuma nacin Saifudddeen kuma itama abuƙace take da mijin nata ga nacin Saifudddeen, dan tunma kafun ta cika wata guda, ya fara mata magana kan cewar yanaso ta karɓi girki, itane dai kawai taƙi, dan tafiso saita yi kwana arba'in da haihuwa, awannan karon bada wasa takeson kamasa ahannunta ba, so take ta gigita duk wani tunaninsa, tayanda saiya manta kansa, hakanne ma yasa da tayi sallan azahar taƙira me zanen jan lalle tazo ta zana mata ahannu da ƙafafunta, yayi mata masifar kyau kuwa,  da kanta tayi driving a dalelliyar sabur motarta zuwa shagon saloon aka wanke mata gashinta,  take ta sake fitowa ɗas da ita, ko Ummi saida ta yaba da irin kyaun da Zaleehan tayi, da ka ganta zaka hango ƙyallin amarci akan fuskarta.

Agaba ɗaya wunin ranan bata yarda sun hafu da Saifuddeen ba, saboda tasan zai iya danneta akowani lokaci.

Koda dare yayi, tana idar da sallan Isha, cikin nutsuwa ta miƙe tare da soma ƙoƙarin shirya kanta,
wata haɗaɗɗiyar net tight gown ta sanya ajikinta, wanda yake dashi gwamma babu, dan ya matuƙar bayyana surar jikinta, wanda suka ƙara cika, hatta shatin nipples ɗinta dake atsatstsaye sun bayyana kansu ta cikin rigan, rigane me tsada da kyawun gaske, dan a Instanbull ta sayo ta, saidai kuma sexy gown ce, ba a sata any how,  sake dogon gashinta da yasha gyara tayi, ya sauƙo har zuwa gadon bayanta,  koda ta kalli kanta amadubi  murmushi tayi, dan ita kanta tasan tayi  kyau,  lafiyayyen  turarenta me tafiya da hankali ta shafa aduk kowani kusurwa najikinta, Masha Allah Ita kanta ta yaba da ƙamshin da takeyi.
Ahankali ta taka ta ƙarasa gaban bedside inda ta aje wayarta, ɗaukan wayan nata tayi, tare da ware wani tattausan meterial me kaman saree ta yane jikinta dashi, cikin wani irin taku ta fita daga ɗakin nata,  kaitsaye sashinsa ta nufa, dan tun da magriba Su Khareem ke gun Inna Shatu, saboda ita ce ke kula dasu ita da Zahira suke kwana dasuma yawanci.

Ahankali ta murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin nasa ta shiga, bakinta ɗauke da sallama, wanda tayisa cikin zazzaƙan muryarta.

Saifuddeen dake zaune agaban computer lumshe idanunsa yayi, sakamakon daddaɗan ƙamshin dayaji ya daki hancinsa, sai kace wanda aka kawo masa kamfanin turare.

Ahankali ya ɗago kansa ya kalleta,  idanunta taɗan lumshe tare da sakar masa wani irin murmushi, samun kansa yayi da miƙewa ya tako zuwa  gareta, idanu suka zubawa juna, suna me aikawa junansu sexy look me wuyar fassaruwa,  ahankali ya ware hannayensa, alaman ta shigo jikinsa. Cikin wani irin salo ta zare laffayan jikinta, tare da shigewa cikin jikinsa, wani irin hugging sukayiwa juna, tare da sakin ajiyar zuciya me ƙarfi, tsananin wutar so da ƙauna haɗi da zallan kewan juna suke gani acikin idanun kowannensu, azafafe ya haɗe bakinsu waje ɗaya, itama cikin azama ta karɓi lips ɗinsa tana tsotsa.
Cikin tsananin kewa suke kissing ɗin juna, azafafe suke aikawa da junansu saƙo, takowani sassa,   jin ƙafafunsu nason gagaran ɗaukansu ne yasa suka zube akan aljannar duniyar gadon nasa,  jikinsu gaba ɗaya rawa yake, haka ya jawota jikinsa, tare da sanya hannunsa ya cire rigar jikinta, hannunsa har ɓari suke alokacin da idanunsa sukayi masa tozali da tsayayyun breast ɗinta, cikin shauƙi yakai hannunsa yana shafasu,  wani irin nishi suke sauƙewa atare ganin bazai iya jurewa ba yasashi ɗaura bakinsa akan breast ɗin nata yana sucking na hikima yadda bazai zuƙo ruwaba.
Cikin shiɗewa ta tura hannunta cikin gashin kansa, tana wasa dashi, kana tana sakin wani irin nishi.
Duk sun zautar da kansu, sun fita hayyacinsu,  gaba ɗaya basa cikin nutsuwarsu,  cikin azama ya shumfuɗeta akan gadon, tare dabin kowani sassa na jikinta da zazzafan kiss,   lokacin da taji sauƙan bakinsa akan privet part ɗinsa, saida ta shiɗe dan wani irin abun da taji na ratsata, yana fara sucking ɗinta ta soma sakar masa gurnani, haɗi da sambatu,
sun gigita junansu ƙwarai,  saida jikinsu ya soma ɓari, kafun ya shigeta, lokacin daya samu kansa acikin jikinta kuwa wani irin ƙara ya sake, wanda babu makawa idan da akwai wani afalo sai ya jiyosu, dan dagashi har ita ɗin babu wanda bai fasa ihun daɗi ba,   tun sunayin abun da kamar wasa har gurnaninsu ya soma zama kuka, da kuma shidewa, sambatu suke wanda su kansu basu san me suke faɗa ba, haka ma Saifuddeen, wani zubin ya yayi sambatun nasa adai-dai wani zubin kuma sambatun nasa sai yayi kama da wani yare na daban.
Gaba ɗaya gurnaninsu ya cika ɗakin, dan Saifuddeen jinsa yake kaman yana firewa asararin samaniya.
Tun Zaleeha nasa ran zai barta, harta cire rai dan sam bataga alaman zai ƙyaleta hakanan ba, abu kamar wasa haka yaƙi barinta ta huta har saida yayi 3 releasing ajikinta, batare daya matsa konan da can ba.
Koda ya sarara mata da ƙyar take iya motsa cinyoyinta, dan har wani zafi takeji, saboda tayiwa kanta gyara bana wasa ba haɗin sa buzu kuwa in kina buƙatan ki tuntuɓeni ta wannan number 09097853276 haɗin masu jego dana amare dana maida tsohuwa yarinya akwaisu seti-seti.
Saifuddeen kam ƙam-ƙam ya rungumeta yana zuba mata kiss takota ina,  cikin shauƙi yace.
"Thank you so so much Zumana, tabbas kedin ta dabance, kinfi zuma zaƙi haka kuma kinfi suga zaƙi, kin kuma fi zaƙin kansa zaƙi, wayyo Allah na, inajin kaman kaina zai buga, kinjiyar dani wani daɗi da bazan taɓa mantashi ba a duniya Inasonki Matata Inasonki sosai kinada daɗi".
Cikin sassanyar murya dake ɗauke da zallan gajiya tace.
"Nima Inasonka Hamma Saif dina, saidai yau ka gajiyar dani da yawa."

Murmushi yayi,tare da ɗaukanta  caɗak suka wuce bathroom, wanka sukayi, sannan ta lafe ajikinsa, haka ya naɗota a towel kaman ƴar baby, gyara musu bed ɗin yayi, dan gaba ɗaya wancan bedsheet ɗin sunyi fatali dashi, Zaleeha ta zubar da ruwa kaman fanfo dan tasha garin maɗi dana mallaka da tsumin igiyar ruwa, shikansa ya shaida Zaleeha ta dabance, dan daya shigeta zai ji kaman acikin kogi yake, saboda yawan ruwan daɗin da take dashi.

Kwanciya sukayi lub ajikin juna, sai kalamai masu sanyaya zuciya suke faɗawa junansu, kowa burinsa shine yafaranta ran ɗan uwansa, yana ta zuba mata kalamai haka bacci ya ɗaukesu.

Washegari  kuwa yana dawowa daga sallan asuba ya sake liƙe mata, wani daɗin suka sake jiyar da junansu, wanda yasa Saifuddeen kuka da hawayensa, ya gigice matuƙa, dan har yanajin kaman Saif ɗinsa zata bar jikinsa ta koma ta zauna a muhallinta.

Suna fitowa awanka ko kaya basu sakaba suka rufawa kansu blanket sai bacci,  har kusan ƙarfe 10  basu farka ba, abu kaman wasa tun su Ummi na zuba idanun ganinsu hardai sukayi jigum, Inna Shatu ne ta haɗawa yaran madara suka sha, dan kowa yasan zuwa yanzu Mamansu nacan tare da cingam ɗin mijinta, bai gama tsotseta ba tukun, Ameena ma dake ranan sunday ne bata da aiki, itama tasha mamakin rashin fitowarsu, aranta tace.
"Hmmm yanzu haka yanacan yana ta zuba mata sambatun da ihun daya saba mata idan suna sex bare yanzu na lura bakinshi ba sakata tunda jiya saida na rufe mishi baki."

Ƙarfe sha ɗaya dai-dai suka farka daga baccin daya ɗaukesu, sosai suka sha mamakin lokacin da suka kwashe suna bacci, atare suka sakeyin sabon wanka, sannan ya tayata ta shirya kanta cikin wani tsadadden lace me adon duwatsu, tayi kyau sosai sai baza ƙamshi take, shima part ɗinsa ya wuce ya kimtsa kansa, suna riƙe da hanun juna suka nufi sashin Ummi, itakam Zaleeha gaba ɗaya kunya takeji, dan batasan me zata cewa Ummi ba, danma tasab su Khausar ba  kuka zasuyi.
Afalo kuwa suka samu su Ummin zaune, tana rungume da Khausar Khasim kuwa yana wajen Inna Shatu, sai Khareem dake wajen Hayatuddeen, dan sun shaƙu sosai kowa ya ɗaukeshi zai amsheshi yace wannan nasane  Hayatuddeen dan ko kuka yake da zaran ya ɗaukeshi yayi jijjigashi yana mishi surutai take zaiyi shiru, yana son Khareem sosai dan kamanshi da yaron kullum ƙara fitowa yakeyi.

Aƙasan carpet Zaleehan ta durƙusa cikin, girmamawa ta gaishe da Ummi.
Fuska asake Ummi ta amsa mata, haka ma ta gaishe da Inna shatu, da kuma Ameena, suma fuska asake cikin fari'a suka amsa mata.
Adeel dake jikin Ameena ne ya taso da gudu ya faɗa jikin Zaleehan, cikin maganarsa ta yara yace.
"Goodu Morying Ammina."
Dariya suka yi dukansu, dan abun ya basu mamaki, cikin farinciki Zaleeha ta rungumesa da kyau ajikinta, fuskarta ɗauke da murmushi tace.  "Wow ashe yarona ya girma har ya fara iya turanci, lallai kuwa dole ne asamin kai amakaranta."

Murmushi Adeel ɗin ya mata har saida dimples dinsa suka lotsa.
Cikin gwarancinsa yace. "Eh Ammina asani a school."
Kansa ta ɗan shafa tare da cewa.
"Okay zan faɗawa Abbanka Insha Allah Za'a saka kaji mangana." Kansa yajinjina mata alaman to kana yana shafa kan Khausar da Ummi ta miƙo mata tana bata nono.

Saifuddeen kuwa akan kujeran dake facing ɗinta ya zauna, sai satan kallonta yake, yanamejin wani irin farinciki da shauƙi acikin ransa, su Ummi kam duk suna lure dashi, dan kallo ɗaya zaka masa kafuskanci cewa yana cikin tsananin farinciki.
Haka dai suka ɗan taɓa hira kafun kowa ya watse, Zaleeha itakam taga ta kanta, dan koda akayi sallan azahar Saifuddeen dawowa yayi, ya gurjeta son ransa, sam yakasa haƙuri da wannan daɗin nata, shi baiƙi acema su tabbata a irin moment ɗin ba.

Kwana biyu da gama arba'in ɗin Zaleeha Saifuddeen ya kamowa Ameena, haka nanma yayi ta sha'aninshi cikin nasu salon shida Ameena'n, kwana biyunta na cika ya kuma dawowa wajen Zaleehansa suka sake sabon raƙashewa...

*******

Kwanci tashi babu wuya, haka rayuwa ta miƙe abubuwan al'khairi da yawa sun faru, dan yanzu watan Zaleeha bakwai da haihuwa, zuwa yanzu yaranta sun ƙara girma sosai sun zama gwanin ban sha'awa dasu, sun ƙara kyau gasu farare sol, har wani yellow yellow skin ɗinsu keyi. Ɓangaren Zaleeha ma, Masha Allah ta nasamun kyakkyawan kulawa daga wajen Saifuddeen sosai, har yanzu kuwa Inna Shatu bata koma ba, dan sosai take taimakawa Zaleeha wajen kula da yaran, kuma ba laifi yaran sun shaƙu da ita sosai.

Ameena kuwa yanzu cikinta ya girma tayi wani dib-dib da ita gwanin sha'awa.
Haka Ziyada itama cikinta ya girma, sosaima.

A cikin watanni bakwa nanne kuma Mudassir abokin Saifudddeen ƙanin Ya Adnan kenan suka ƙulla soyayya shida Zahira, cikin ƙanƙanin lokaci akayi aurensu.

Hakama ɓangaren Babansu wato Saifuddeen Alhamdulillah rayuwarsa yake cikin jin daɗi, idan ka gansa bazaka taɓa cewa adacan baya shi kurma kuma gurgu bane, ya sake zama wani handsome dashi, ya zama wani babba na musamman, afannin aikinsa kuwa bakaɗan ba yake ƙokari, hakanne ma yasa aka ƙara masa Matsayi.
Yanzu ya zama babba, wanda yaune kuma za ayi liyafar ƙarin girman nasa, hakanne yasa yau tun safe gidan suka tashi da shirye shiryen zuwa liyafan, ba kaɗan ba sukaji daɗin karin girman da akayiwa Saifuddeen din.
Ameena da Zaleeha shirya kansu sukayi cikin wani tsadadden lace wanda Saifuddeen ɗinne ya saya musu, iri ɗayane lace ɗin saidai banbancin kala, sun matuƙar yin kyau bana wasa ba, inda yanzu cikin Ameena ya girma dan yana da kusan watanni shida kenan.

Kowa ya kimtsa kansa, haka ma su Adeel da ƙannensa Khareem, Khasim, Khausar, suma shiga me kyau akayi musu, Ummi da kanta wani haɗaɗɗen lace ta saka, wajen zuwa liyafan kuwa harda Raleeya wanda itama tasha ado cikin wani tsadadden lace da Ahmad ɗinta ya saya mata, cikin wasu zafafan motoci suka shiga sannan suka tafi zuwa wajen liyafan, gaba ɗaya abokansa sun samu hallaran wajen da matayensu, su Ishaq da Rasheeda ma sun taka rawar gani sosai, Zakariyya da Hayatuddeen dasu Khamis da Imran Isma'il Sulaiman ma sun halarci wajen, duk sun sha kayansu masu kyau da tsada, ga Adda Rahama da kuma Ya Adnan ma da yaransu suma sun samu zuwa.
haɗaɗɗiyar liyafa aka gudanar wanda akaci akasha, sosai abun ya kayatar, daga kan Zaleeha zuwa Ameena babu wacce bata fita tayi godiya akan high table ba, kowa yasha mamakin ganin zankaɗa zankaɗan iyalan Saifuddeen din, musamman ma Zaleeha dan irinsu sunfi kama da matan shugaban ƙasa.
haka dai aka kare liyafan cikin jin dadi da nishaɗi, daganan kuma suka dawo gida.

Ɓangaren kasuwancinsa ma Alhamdulillah akwai nasara sosai da kuma samun cigaba, abun saidai ace Masha Allah, dan na sarorin rayuwa kam anasamunsu, gashi suna samun tsabtatacciyar riba, wanda babu algus acikinta.
Tuni an warewa Hayatuddeen tumin gadonsa da dukiyarsa da ribarsa gaba ɗaya haka su Adda Rahma da Raliya da Raihana.
Kowa yasan tarin dukiyarsa ana kula da komai da taimakon Bello Ahmad da Mudassir da Warisu wanda zuwa yanzu ya zama ƙaton mutun mai teɓa yana ta gudun ƙibar dai kuma bai tsiraba.

By
*GARKUWAR FULANI*

LITTAFIN nan na kuɗine biya ɗarinki uku kacal ki karanta ba tare da haƙƙin kowa ba a kanki, turo katin mtn na ɗari uku ta wannan layin 09097853276 ko kiyi min transfer ɗari uku ta asusuna na 0005388578 jaiz bank Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo shaidar biyanki. Ga masu buƙatan kayayyakin gyara na mata akwai masu kyau da inƙanci in kina buƙata domin shirya amarya ko mai jego ko maida tsohuwa yarinya ki tuntuɓeni ta wannan layin 09097853276...

Godiya ta musamman a ga ƙungiyar nakasassu ta Gombe Joint national association of person's with disabilities (Jonapwd) Gombe state chapter All the best!👍🏻👌🏻 Inai muku fatan al'khairi da fiye da yadda kukemin ngd ngd ngd matuƙa da karramarku gareni Malam Ishaq inayi maka fatan al'khairi, Hajia Zaleehan Hamma Saif inai muku fatan Al'khairi a rayuwarku, baki bazai iya godiya bisa al'khairinku gareni ba. Allah ne zai biyaku ni dai sai dai inyi ta muku addu'a.

Wannan shafin nakane mai sunan Babana Ali Wambai Happy birthday 2 you, inai maka fatan

al'khairi a rayuwarka ta duniya da ƙiyama.

Daga wajen liyafan kaitsaye gida suka dawo, zuciyarsu cike take da zallan farinciki, tabbas sun samu nasarorin rayuwa ƙwarai, komai saidai suce. Alhamdulillah. Yau Zaleeha ne da karɓan girki tun da safe kuwa ta karɓi baƙoncin Rashida, sosai taji daɗin zuwan Rashidan, anan falon ta suka zauna. Cikin salon tsokana Zaleeha ta dubi Rasheedan, fuskarta ɗauke da murmushi tace. "Matar makaho yadai naga sai wani fresh kikeyi ne? kodai kodai ƙwallon mutumin namu yashiga raga ne?". Dariya Rasheeda tayi tare da watsa mata hararan wasa, gyara zamanta tayi tare da cewa.

"Ohon miki dai, ai koma mene ke zan tambaya, tunda kece kullum jikinki fresh saikace irish patatoe."

Dariya sukayi su dukansu, Zaleehan ne tace.

"Hmmm ni duk ba wannan ba, zo kimin lalle dan Allah, rabona da lalle yaɗan jima, waima kin sakejin labarin Balkeesu kuwa?". Murmushi Rasheeda tayi tare da cewa.

"Bansake jin labarinta ba kwata-kwata, gaskiya ƙarshen Balkeesu baiyi kyauba, da kanta ta ɓata rayuwarta, Allah dai yayi mana me kyau."

Da. "Ameen". Zaleeha ta amsa, dan itakan tabbas Balkeesu ta cutar da ita arayuwa, guduwan da tayi tabar ɗakin aurenta, akwai sa hannun Balkeesu aciki dumu dumu, amma gashi tun aduniya Allah ya mata sakayya.

Hira suka ci gaba dayi da Rasheedan, wanda duk bayan mintuna kaɗan saitaje ta zubar da yawu a sink, ita kuma haka nata salon cikin yazo, bata rabuwa da yawu abakinta, da ta gaji datashi ne, Zaleeha ta bata sweet ta jefa abakinta, bayan Zaleeha ta kawo mata kayan ciye ciye taci ne, tayiwa Zaleehan zanen lalle me kyau.

Har yammaci Rasheeda takai agidan, saida sukayi sallan magriba kafun Ishaq yazo ɗaukanta, Ummine ta sashi agaba saida yaci abinci ya ƙoshi sannan ya ɗauki Rasheedan suka tafi. Zaleeha kuwa koda aka idar da sallan isha, sabon wanka tayi tare da tsantsarawa kanta ado, sosai tayi kyau cikin shigar sleeping gown ɗin da ta sanya. Sai ƙamshi take bazawa haka ta nufi sashin Saifuddeen.

Inda su Khareem da Khausar kuwa suke wajen Inna Shatu, kasancewar sun ƙara wayo hakan yasa, basu da wani yawan ƙiriniya, sosai suka saba da Inna Shatu shiyasa idan zasu wuni su kwana awajenta, matuƙar sunsha nono to bazasu taɓa yi mata kuka ba, ga kuma Baffan su Hayatuddeen wanda shima ya ɗauki nauyin kula da yaran akansa, dan da zaran ya dawo school yana gama karatunsa, zaizo ya ɗaukesu dukansu haka zai kwanta acikinsu yana Musu wasa. Da sallama ɗauke abakinta ta shiga cikin ɗakin nasa, fitowarsa daga wanka kenan dagashi sai towel ɗaure a ƙugunsa.

Murmushi suka sakarwa juna, atare suka kashewa juna ido, giransa ɗaya ya ɗaga mata alaman. "Babe ya?." ƙarasowa gaban dressing mirror'n tayi, ɗan ƙaramin towel ta ɗauka ta shiga goge masa jikinsa, yanayin yanda take goge masa nasa jikin da salo ne, yasa duk yaji jikinsa ya sake, Saif ɗinsa na ƙoƙarin miƙewa, ganin haka yasa ta ware towel ɗin dake jikinsa, ahankali takai hannu ta shafo Saif dinsa, wanda take ta tsaya cak, cikin wani irin salo ta soma shafasa tana ɗan murzawa ahankali, ganin yanda tsikar jikinsa suka mimmiƙe ya kuma wani lumshe ido, yasa takai bakinta kan Saif ɗin, take ya saki wani irin nishi da kuma gurnani,

hakanne yasa ta soma yi masa sucking tana lashewa da harshenta,  sosai ta zautar dashi, har ƙafafunsa suka garara ɗaukarsa.
Ahaka yajata suka karasa kan gado, light off ɗin wutan ɗakin ya musu,  azafafe ya rabata da kayan jikinta.
Wani irin romancing suka shiga yiwa juna, wanda yasa duk jikinsu ya ɗauki rawa, lokacin da suka samu kansu ajikin juna, wani irin nishaɗi ne ya ziyarcesu, haka suka dinga sambatu da gurnani kala-kala,  sun raya daren nasu cike da soyayyar juna, yayinda Saifuddeen ya more zuman Zaleeha son ransa, bayan sun dawo cikin nutsuwarsu ne sukaje sukayi wanka, koda suka kwanta maƙale da juna haka sukayi bacci.

***

Lokuta da dama rayuwa tana tafiya, kwanaki suna gushewa, abubuwa kuma da yawa na faruwa, to hakanne yakasance arayuwar su Saifuddeen dan yanzu Shekaran Zaleeha Ɗaya cib da haihuwan su Khareem, acikin Shekara ɗayan nan kuma da ta wuce abubuwa da yawa sun faru, ciki kuwa harda haihuwan Ameena inda ta sake haifo ɗanta Namiji, mai kama da ita sak, saidai farin Babansa ya ɗauko,  anyi shagali asunan nata masha Allah, Saifuddeen yayi bajinta, ankuma sakawa yaron sunan Babanta,  taji daɗin hakan kuwa sosai suna kiranshi Abbi.
Yaran Zaleeha kuwa masha Allah sun ƙara girma sosai, sun zama gwanin ban sha'awa, dan har sun soma takawa da kafafunsu, duk dama tafiyan beyi ƙwari sosai ba, saidai wani abun mamaki yaran sun taso da wani irin kyawun daya zarce na iyayensu, hakanne yasa kowa ke so da ƙaunarsu,   babuma kaman Babansu, Adeel ma yasake girma sosai dan har ansashi a makaranta, sosai ya ƙarayin wayo,  ɓangaren shaƙuwansu da Zaleeha kuwa sai abun da yayi gaba, dan hatta kayan sawanshi yanzu a sashin Zaleehan yake, bashi da wani magana saina Amminsa, komai nasa na Amminsa ne, soyayyace me zafi atsakaninsa da Zaleeha.

Ziyada ma ta haifi ƴarta mace, wanda akayiwa Adda Maryam takwara, za'ana ƙiran yarinyar da sunan  IMAN,  tasha gata kuwa awajen ƴan uwa da mijinta, dan hidima sosai suka mata.

Haka Rasheedan Ishaq ma ta haihu, ta samu ɗanta namiji, wanda aka mawa Saifuddeen takwara, ranan da Saifuddeen yaji cewa ɗan Ishaq ɗin takwaransa ne baƙaramin daɗi yaji ba, haka ma su Ummi sun tayasa murna.

Aɓangaren Hayatuddeen dasu Zakariyya kuwa karatunsu ya miƙa, kuma Alhamdulillah suna samun nasarori acikin karatun nasu sosai, dama shi Hayatuddeen ɓangaren Accounting yake karanta, dan bashi da wani buri da ya wuce zama cikakken ma'aikacin banki, shikuwa Zakariyya Low yake karanta, dan burinsa ne zama babban lowyer me zaman kansa,   Khamis kam aɓangaren Doctors yake, wanda kowa acikinsu yanason burinsa yakai ga ci.    Alhamdulillah kuma suna samun nasara, dan kowanne sakamakonsa yana fitowa da kyau, dan ko a exam ɗin da sukayi, Hayatuddeen shi yazo second class offer,  sosai sukayi farinciki, hakanne ma yasa Saifuddeen ya basa mota, wanda zaina ɗan zirga zirgansa aciki,  yaji daɗin hakan kuwa, dan dama Ya Ahmad ya sayawa Zakariyya mota me kyau, Khamis ma kuma dama yana da nasa motar.

Yau dai kam Hayatuddeen ya ƙudurta aransa cewa zai sanar da Hammansa game da maganan Zahrah, dan zuwa yanzu sunyi wani irin sabo da Zahrah'n duk dama tanajin kunya da nauyinsa, bata wani sakewa dashi, amma tabbas ya hango zallan ƙaunarsa acikin idanunta,  sannan kuma akullum yanajin kansa abuƙace da mace, dan zuwa yanzu yana da kusan shekaru 24 kenan, duk dama bayanzu yakeson auren ba, ya fiso sai ya kammala school ɗinsa zuwa lokacin yasan yana da 26 years.  Koda ya samu Hamman nasa da maganan Zarah, sosai Saifuddeen ɗin yasha mamaki, saidai bai nunawa Hayatuddeen ɗin ba,  murmushi ne ya fafaɗa akan fuskar Saifuddeen ɗin, cikin kulawa yace.
"A ina yarinyar take? sannan kuma a ina kuka haɗu da ita? a ina kuma iyayenta suke?."
Duka waɗannan tambayoyin yayiwa Hayatuddeen su, bayan ya zuba masa tsumammun idanunsa.       Ɗan sosa ƙeya Hayatuddeen yayi cike da kunya, cikin ɗan basarwa yace.
"Sunanta Zarah Hamma, kuma agidan Baba Bello take, ƴar ƙanwar Baba Bello ne, mun haɗu da ita tun wani zuwa da nayi, lokacin kuna Instanbull, ka aikeni nakai masa kuɗi shine muka haɗu da ita, Allah Hamma saif yarinyar tanada hankali sosai,  kuma a layin gomnan Yobe gidansu yake".
Murmushin jin daɗi Saifuddeen ɗin yayi, cikin gamsuwa da kalaman Hayatuddeen ɗin ya jinjina kansa, tabbas yaji daɗin hakan, Insha Allah kuma bazai ƙi nemowa Hayatuddeen ɗin auren Zarah'n ba, duk da yasan cewar Hayatuddeen ɗin nada rikici, amma kuma bazai yiwa kansa zaɓin dabai dace dashi ba.         Gyara zamansa yayi, cikin nutsuwa yace.   "Naji daɗin hakan.ƙwarai,  na kuma yi farinciki jin cewar ɗiyar Baba Bello ce, dan babu wani wanda zaiso ƙin haɗa zuri'a da jinin Baba Bello, tabbas Baba Bello mutumin kirkine Insha Allahu kuma, nasan zaiyi mana jagora wajen zuwa tambayo maka auren Zarah awajen iyayenta, saboda haka ka kwantar da hankalinka, Insha Allah ko zuwa gobe zanyiwa Baffa Ali magana, duk abuk dayace shikenan."          Cikin jin daɗi Hayatuddeen ya rungumi Hamman nasa, cike da zumuɗi yace.
"Nagode sosai Hammana, yanzu zanje na faɗawa Ummi komai."   Murmushi kawai Saifuddeen yayi, Hayatuddeen kuwa da sassarfansa ya nufi sashin Ummi.
Ummi ne kaɗai afalon sai kuma Zaleeha wanda take kwance asaman doguwar kujera, su Kareem da Khasim dama suna can wajen Inna Shatu.       Ƙarasowa cikin falon yayi yana ta sakin murmushi, jin zuciyarsa yake fara ƙal,   ganin yanda yake ta sakin fari'a yasa Ummi cewa.
"Hayatuddeen wannan fara'ar taka kuma ta mecece, duk yanda akayi dai akwai abunda kasamu na al'khairi."      Murmushi yayi tare da zama akusa da Ummi'n nasu.
Hannayenta ya kamo ya riƙe cikin nuna tsantsar ƙaunar da yakewa Zarah yace.
"Ummi kin tuna lokacin dana kaiwa Baba Bello aika, lokacin su Hamma suna Instanbull?".
Ɗan jim Ummi tayi, tunowa da ranan yasa ta jinjina kai alaman. "Eh"           Murmushi ya kumayi tare da cewa.
"Yauwa to Ummina, arananne na haɗu da wata ƴar ƙanwar Baba Bello, Wallahi Ummi yarinyar tana da hankali ga nutsuwa, kuma sunanta Zahrah, ummmm to shine fa dama tun alokacin naji..."   Shiru yayi yana wani ɗan sunne kai alaman kunya.    Dariya Ummi tayi tare da cewa.
"Ikon Allah wai yau kuma ni Hayatuddeen kejin kunya, lallai akwai wata aƙasa, faɗamin kaji autana inajinka."
Jin haka ne yasa shi sake nutsuwa, duban kansa yayi, tare da cewa.    "Ummi ranan ina cewa kikayi na girma ko."          Kai Ummin ta jinjina masa tana murmushi tace.

"Ai yanzuma kafi ranan girma, yanzu fa kai saurayine bakaji na daina ce maka Autana ba, saboda ka girma ne ai."   Jin kalaman Ummin yasashi jin sanyi aransa, tare da sabon ƙwarin guiwa.
Cikin zumuɗi yace.  "Yauwa to Ummi, dama tun aranan naji inason Zarah'n, kuma naje gidansu gaishe da Mamanta ma yafi sau uku, kuma itama nafahimta tana sona, tun alokacin muka fara soyayya, saidai banason faɗawa Hamma karyace nayi ƙarami, shiyasa na bari sai yanzu na faɗa masa, kuma yayi na'am yace zai faɗawa Baffa Ali sai su samu Baba Bello, Inason abani ita agidansu Ummi, kinga yanzu next month zan fara bautan ƙasa, dana gama kuma shikenan nasan zan samu aiki,  daganan kuma ai Ummi kinga zan iya aure ko?".
Wani irin farinciki ne ya cika zuciyar Ummi, tabbas taji dadin hakan,  musamman ma jin cewa ita yarinyar kamar ƴa take awajen Baba Bello, tsohon arziki.
Kansa Ummi ta shafa cike da gamsuwa tace.  "Masha Allah Autana ya girma, na kuma ji daɗin wannan zancen saboda haka Allah Ya sanya al'khairi  ya kuma sa itaɗin rabonka ce."
Da.  "Ameen" ya amsa yanata wani jin daɗi.  Idanunsa yakai kan Zaleeha dake bacci, hannunsa yasa yaja Khausar dake jikinta,  cikin zumuɗi yace.  "Adda Zaleeha wakeup please, nazo da labari me dadi."
Zaleeha da baccinta baiyi wani nisaba ta buɗe idanunta, ganin Hayatuddeen ne yasa ta tashi ta zauna tare da kontar da Khausar.      Hayatuddeen kam zumuɗi yakasa barinsa yayi sakat, hannu yasa yana shafa kan Khausar kaman yanda yayiwa Ummi haka ya shiga bata labarin Zarah.
Sosai Zaleeha taji daɗin hakan, take ma taji baccin nata ya gudu, nan ta biye masa suka shiga hiran Zarah, ita da kanta take tsara irin yanda bikin na Hayatuddeen zai kasance.
Dubansa tayi cike da farinciki tace.
"Lallai lokaci yayi Hayatuddeen, tabbas kowa sai yashaida auren Autan Ummi, zamuyi ɓarin daloli zakuma mushiga mu fita, insha Allah bikinka sai ya zama abun kwatance agarin Gombe, zamu nuna maka gata sosai, wani abun saima awajen diner  party, ni dakaina zan fitar mana da ankon tsalelen lace."
Murmushin jin daɗi Hayatuddeen yayi, tare da cewa.
"Yauwa Adda Zaleeha shiyasa nake sonki ai."  Hira suka cigaba da ɗan taɓawa, kafun daga bisani ya ciro wayarsa ya ƙira Raleeya,  tundaga kan farkon haɗuwarsa da Zarah har zuwa yanzu saida ya labarta mata, sosai taji daɗi take itama tasoma juyi da imagine yanda zasu tsara bikin.      Hira suka ɗan taɓa shida Raleeyan kafun daga bisani sukayi sallama.

Haka dai  Hayatudeen ya ƙare wunin ranan na yau, cikin farinciki da zumuɗi.   Ɓangaren Saifuddeen kuwa, tun ayau ɗin ya ƙira Baffa Ali ya sanar masa abun da Hayatuddeen ɗin yazo dashi, sosai kuwa Baffa Ali yaji daɗin hakan, yayi farinciki matuƙa, nan yake cewa Saifuddeen ɗin.
"Insha Allah gobe zaizo idan yaso sai suje can wajen Baba Bello'n dan ya sama musu iso wajen iyayen Zarah'n."
to ahaka dai suka tsaida magana.

Koda dare yayi bayana an idar da sallan Isha, Saifuddeen sashin Zaleehansa ya wuce, kasancewar yau itace dashi, dan Ameena ma batanan yau tana da Night duty, kuma awannan

karon bata barin yaron nata agida, dashi take tafiya, dan yana da yawan kuka, shi bakamar Adeel bane da yake babu ruwansa, gashi yaron yana da yawan tsotso.

Koda ya shiga ɗakin Zaleehan tsab ya sameta, ta kimtsa kanta cikin wani body hug masu kyaun gaske, wanda suka bayyana zallan suran jikinta. tana ganinsa taje ta faɗa jikinsa, tare da saka masa sakalci wai ita dole ice cream zata sha, wanda yake cikin fridge ɗinta kuwa ya ƙare. Hannunta ya kama suka nufu side ɗinsa, shida kansa ya ɗauko ice cream acikin fridge ɗinsa, zaunar da ita yayi akan cinyoyinsa. Ahankali yake bata ice cream ɗin abaki, tana sha tana lumshe masa fitinannun sexy eyes ɗinta, wanda yasa yaji gaba ɗaya ya fara rasa nutsuwarsa. Ganin irin kallon da yake binta dashi, yasa ta haɗe bakinsu waje ɗaya, tana me bashi wani irin lafiyayyen kiss, sanyi da daɗin bakinta daya ratsashi ne yasashi sakin wani zazzafan nishi. Haka suka dinga kissing juna cikin salo, daga nanne kuma labari ya sanja salo, inda suka nutsar da kansu cikin wata daddaɗan duniya na musamman wanda yasasu zaucewa da sambatu.

Bayan sun nutsune suka maƙale juna, ahankali yake shafa bayanta har tayi bacci, tashi yayi ya ƙarasa aikinsa daya fara tunda yamma amma baiƙarasa ba, da yakeyi, yana kammalawa yazo ya kwanta ajikinta shima haka yayi bacci.

Washegari Kamar yanda Baffa Ali ya faɗa cewar zaizo, bayan anyi sallan Azahar kuwa sai gashi yazo.
Basuje gidan Baba bellon ba kuwa saida sukayi sallan La'asar, bayan sun idar da sallan ne suka tafi. Aƙofar gida suka samu Baba Bello, ganinsu yasa yaji daɗi, ya kuma yi musu tarba ta musamman, anan cikin ɗakinsa dake zaure ya musu masauƙi. Iya ne ta kawo musu ruwa me sanyi da kuma fura, duk da cewar Saifuddeen aƙoshe yake, amma saida yasha sosai, dan baya taɓa iya tsallake tayin gidan Baba Bello, dan ko ba komai nan ɗin ji yake kaman gidansu ne, haka ma Baba Bellon matsayin Baba yake agaresa. Gashi kuma yasan Iya ta ƙware sosai wajen dama fura kindirmo.
Bayan sun gama shan furanne, Baffa Ali yayiwa Baba Bellon bayanin komai.
Jin abun daya kawosu yasa zuciyar Baba Bello tayi fari, take ya cika da murna, dan kusan shi ya mafi kowa jin daɗin hakan, dan tabbas yasan Hayatuddeen yaro ne me hankali, gashi kuma yana da tsatso da kuma nasaba me kyau, saboda haka wa zaiƙi haɗa jini dasu.
Cikin son ƙarafafa musu guiwa da kuma amincewa yace. "Tabbas naji daɗin wannan maganan na kuma yi farinciki, saboda haka insha Allah yau basai gobe ba, zan nema muku izinin ganawa da iyayen Zara'u, nakumasan mahaifinta bazai ƙiba, dan me biyayyane agareni."
Godiya sukayiwa Baba Bellon, take kuwa ya ciro waya ya ƙira Alhaji Ibrahim wato Baban Zarah'n kenan.
Shaida masa yayi cewa. "Anjima idan ya basu lokaci zaizo shida baƙi, zasu zo roƙon iri awajensa."
Babu wani kwana kwana ko jan lokaci Alh. Ibrahim ɗin yace.
"Su zo koda yaushe yana maraba dasu." sunji daɗin hakan ƙwarai sun kuma saida lokaci cewa, idan suka idar da sallan Isha zasu zo sai su ɗauki Baba Bellon zuwa can gidan.
Hakan kuwa akayi koda sukayi sallan Isha, gidan Baba Bello suka sake komawa, bayan sun

ɗaukeshi ne kuma suka nufi unguwar su Zahran. Koda suka ƙarasa gidan, tarba me kyau suka samu daga wajen Alh.Ibrahim mutumin arziki wanda ya iya karrama baƙi, dan anan cikin babban falonsa ya sauƙesu, yaji daɗin ganinsu ƙwarai, koda yaji abun da yake tafe dasu kuwa, farincikin nasa ƙara ninkuwa yayi, dan suɗin mutanene masu mutumci, bakuma wanda zaiƙi jininsu, dan yasan Saifuddeen yana kuma jin labarinsa awajen Baba Bello, harma dasu Alhaji Ishaq, dan Alhaji Ishaq da Alhaji Kabiru abokan sana'ansa ne, suna ɗan taɓa harkan saya da sayarwa ga junansu, dan shima ɗan kasuwane me cikakken rufin asirin Allah, dan sam bazaka ƙirasa da talaka ba, bakuma zaka ƙirasa da irin masu kuɗin haukan nan ba, saidai kuma akomai nasa babu ƙaranta. Kasancewar shida ƙaninsa me bi masa ne, suka tarbi su Saifuddeen ɗin, hakan yasa basuyi wani dogon zanceba, sukace sun bawa Hayatuddeen Zarah, insha Allah idan da rabo zata zama matarsa,dan dama yarinyar karatu take bata kuma kula kowa, bata ma taɓa tsayuwa da kowa da sunn hira ba, amma sun bawa Hayatuddeen daman yana zuwa zance, saidai kuma sun roƙi alfarmar cewa, abari saita ƙarasa karatunta kafun akawo maganar aure gadan gadan dan yanzu saura mata shekara biyu na ne ta gama secondary school. Sosai su Saifuddeen sukayi na'am da hakan, dan suma sun fison hakan, ko ba komai zuwa lokacin Hayatuddeen ya kammala bautar kasan sa, sannan kuma harma ya kama aiki Insha Allah. To ahaka dai suka tsayar sun kuma yi magana ta fahimtar juna masha Allah kuma, zuciyar kowa fari tas take, sun rabu da juna cikin aminci da mutuntawa.
Koda suka dawo gida, basu ɓoye komai ba suka sanar da Ummi, sosai taji dadin hakan, ta kuma ƙara godewa Allah, da nasarorin rayuwa da yake basu. Hayatuddeen ma dake laɓe duk yaji komai, haka ya dinga tsalle da rawan murna, har yanaji ajikinsa cewa shikenan ya gama mallakan Zarah, Insha Allah Zarah tasa ce. Haka su Saifuddeen suka ƙirasa suka sanar masa komai da Baban Zarah'n yace.
Yayi na'am da hakan shima, saboda yasan hakan al'khairi ne agaresu, domin shima bayaso ya ɗauko maganan aure batare daya fara aiki ba, so yake shima ya tsaya akan kafafunsa, kaman yanda Hammansa ya jajirce wajen samarwa kansa dukiya ta halak, haka shima yake fata, bayason ya dogara da kowa da kansa yakeson tsayawa akan ƙafafunsa, duk da yasan cewa shiɗin me gata ne gaba da baya, amma hakan bazai sa ya kashe zuciyarsa ba, amatsayinsa na Namiji dole ne agaresa ya nemi na kansa.

Alhamdulillahi yau tsawon sati guda kenan da nemawa Hayatuddeen izinin fara zuwa zance gidansu zarah, kuma ayaune jumma'a yakeson zuwa gidan su Zarah'n. Yau gaba ɗaya abokan nasa suna nan cike agidan su, anan falon Ummi suka baje sai ciye ciye suke, sun girma amma sam wani lokaci halin nasu na yarinta na nan, yanzu ma Zaleeha ne tayi musu farfesun kaji suke ci, sai zuba santi suke, wasu daga cikinsu kuwa tsokanan Hayatudeen suke, acewarsu waidan zai fara zuwa zance yau shiyasa gaba ɗaya yakasa koda zamane, abinci ma ya kasa ci na kirki.
Khamis ne ya dubesa, cikin salon tsokana yace. "Hayatuddeen ango." Murmushi Hayatuddeen ɗin yayi tare da cewa. "Maganarka haka take soon insha Allah". Dariya sukayi dukansu, Imran ne yace.
"Nima dai Insha Allah zan biyo bayanka Hayatuddeen, dan wallahi nima inason aure".
Khamis ne yace.
"Kuji Imran fa, to waye bayason aure? ai kasha kuruminka wata ƙila ma ni na riga Hayatuddeen

aure, dan dama ni suke jira".
Dariya sukayi dukansu,  Zakariyya dake tauna tsokan kaza abakinsa ne yace.
"Dukan ku kallon ku nake dan duk saina rigaku aure, nima ba zama zanyi ba, dole zan faɗawa Baba Malam cewa aje anemamin aure".            Dariya Hayatuddeen yayi tare da cewa.
"Lalle ma guys ɗinnan wato duk kishi kuke dani, dan kawai kunji anbani babe shikenan sai kuka tashi hankalinku, kai Zakariyya kana maganan aure bayan ko budurwa baka dashi."
Murmushi Zakariyya yayi tare da shafa tarin sumar kanshi, cikin jin kai yace.    "Kuna wasa dani guys ɗinnan, tun yaushe kuma na samu matar aure, ko kunason cemin kun manta da Zaytoon ne?"    Idanu Hayatuddeen yaɗan zaro cikin mamaki yace.
"Wai kana nufi Zaytoon beauty kakeso, ƴar fada ce fa".
Dariya sosai Zakariyya yayi tare da cewa.
"Am so what dan ita ƴar  sarki ce, nidai inasonta kuma itama tana sona kuma wallahi Insha Allah Saina aureta, nasan Baba Malam zai shigemini gaba,  kuma kasan age mate ɗin Zarah'n ka ne, dan itama yanzu take shekaranta na kusa dana ƙarshe a secondary school, ni dai kam zama corper yayimin amfani a rayuwata dan yacillani zuwa school me daraja, har na gano gwanata."      Dariya sukayi dukansu, Zaleeha dake jinsu itama dariya tayi, dan tajima da sanin labarin Zaytoon awajen Zakariyya, kasancewar baya ɓoye mata komai nasa, kafun yayi komai saiya faɗa mata.
Hira sukayi sosai.         Haka dai yamma nayi suka watse, Inda ya rage saura Zakariyya shi kaɗai, dan shine zai raka Hayatuddeen ɗin wajen Zarah.
Da Misalin ƙarfe huɗu na yamma kuwa suka nufi gidan su Zarah'n, bayan kowannensu yasha kwalliya cikin tsadaddiyar shadda me kyau.
Koda suka isa gidan su Zarah'n,  har cikin falon Babanta akayi musu iso, saida aka kawo musu kayan taɓawa kafun Zarah'n ta samu isowa, tayi kyau sosai abunta cikin shigar riga da zani na atamfar dake jikinta, inda ta yane jikinta da mayafi me kyau, masha Allah tayi kyau sosai, haka Hayatuddeen ya kasa ɗauke idanunsa daga kanta.
Aladabce ta gaishesu, Zakariyya ya amsa mata fuska asake,  idanu ya kashewa Hayatuddeen alaman zaɓin nasa yayi sosai, sannan ya tashi ya basu waje dansuyi zancen su cikin salama.
Ganin Zakariyya ya fita ne yasa Hayatuddeen ci gaba da kallon Zarah'n yana sakin murmushi.
Jin shirune yasa Zarah taɗan ɗago kai ta saci kallonsa, ganin ita yake kallo yasa ta kawar da kanta gefe tana murmushi. Shiɗin ma murmushin yayi, cikin salon jan hankalinta yace.
"Sannunki da zuwa Amaryata".
ɗago kai tayi taɗan kallesa da mamaki, dan bata tsammaci tun daga yanzu zai ƙirata da sunan amarya ba.
Ganin ta kalleshi ne yasa cikin ƙwarin guiwa yace.  "Yess ke amaryata ce, ko kina musu da hakanne ƴan mata, sarauniyar murguɗa baki".
Dariya ne yazo mata amma saitayi murmushi, cikin ranta wani irin daɗi takeji, dan tabbas ta kamu da soyayyan Hayatuddeen ɗin, dan bakaɗan ba yake burgeta, musamman idan yana juya idanunsa like Hamma Saif, abun yana mata kyau sosai.     Ganin yanda take ta rurrufe fuskane yasa Hayatuddeen  soma yi mata hira,  wani lokaci tayi murmushi wani lokacin kuma maganan nata baya wuce.
"Eh ko a'a".      ahaka dai sukayi hiran ƙarfe 5 dai-dai ya mata sallama ya tafi, koda yazo tafiya ledan da Ummi ta basa wanda yake cike da kayan shafa ya bata, ƙin amsa tayi kwata kwata,

hakanne yasa ya ajiye mata anan cikin falon ya tafi.
Ko acikin mota hiran Zarah'n sukayi shida Zakariyya, ahaka har suka isa gida Hayatuddeen yanata zumuɗi kamar ance masa gibene auren...!

By
*GARKUWAR FULANI*
Littafina na kuɗine biya ɗarinki uku kacal ki karanta ba tare da haƙƙin kowa a kankiba turo katin mtn na ɗari uku ta wannan layin 09097853276.

Koda suka ƙarasa gida kuwa, nan cikin falo suka zauna, tare da soma fara bawa Ummi labarin irin karramawan da akayi musu agidan su Zarah'n, sosai Ummi taji daɗi dan taji ajikinta cewa tayi sa'an surukai na kwarai, saidai fatan Allah ya nuna mana lokacin biki.
Haka dai suka ɗan taɓa hiransu a falon Ummin, kafun daga bisani Zakariyya ya tashi ya tafi, inda Hayatuddeen ya rakasa har waje, saida ya shiga motarsa sannan ya dawo gida.

Tofa haka rayuwa ta kasance, tun daga wannan ranan sai ya zamana duk ƙarshen sati Hayatuddeen yakanje zance gidan su Zarah, Masha Allah kuma dan yasamu karɓuwa sosai awajenta, haka ma iyayenta, tun bata sakewa dashi har ya zamana ayanzu sun zama tamkar wasu abokai saboda shaƙuwa.

Bayan wata ɗaya da bashi zarah ne ya soma service ɗinsa.
Sannu ahankali kuma yake tafiyar da service ɗin nasa yanda ya kamata, dan dukansu acikin Gombe suke service ɗinsu, Khamis da Imran ne kawai aka turasu kudu, amma suma suna ɗan leƙowa gida time to time.
Haka dai rayuwa ta miƙa, kwanaki da watanni na wucewa, yayinda abubuwa da yawa na faruwa, rayuwa tayiwa kowa daɗi.

***

BAYAN SHEKARU UKU. Alhamdulillahi rayuwa ta cigaba da tafiyawa familyn cikin kwanciyar hankali da salama, abubuwan daɗi suna ta faruwa.
Ta ɓangaren Saifuddeen rayuwa ta miƙa masa sosai, budi da alkhairi suna ta shigo masa, ya sake haɓaka yazama babban me arziki da rufin asirin Allah ya tabbata NAKASA BA KASAWA BACE.

Inda acikin shekarun da suka wuce ɗinne, Zaleeha ta koma taci gaba da aikinta.
Ta kuma sake samun ciki ta haifi ɗanta na Miji, wanda yaci sunan Aleeyu, inda akayiwa Baffa Ali takwara, ana kiranshi Haydar.
Ranar da Haydar ya cika shekara biyu ta kuma haifi ƙanwarsa, Wacce Saifudddeen ya yasa

mata suna Aysha, ana kiranta Aish itama yanzu shekaranta ɗaya cib.
Yanzu yaran Zaleeha biyar Khareem Khasim Khausar Haydar autan Aish.
Bayan Zaleehan ta haihu kusan da shekara ɗaya ne Ameena ma ta haifo ƴarta mace me kama da ita sak,
Yayinda yanzu yaran Ameena uku Adeel Abbi Rahma.
farincikin da familyn sukayi nasamun ƙaruwa ba ɗan kaɗan bane.
Ɓangaren su Khareem da Ƙaseem Da Khausar Haydar kuwa sun ƙara girma sosai, yayinda asalin kyawunsu ke ƙara bayyana, zuwa yanzu dukansu babu wanda ba a sakashi a makaranta ba, Khausar kuwa kullum ƙara girma take, ga wani irin fitinannen kyaun da take tasowa dashi, kowa ya ganta saidai kaji yana cewa.
"Masha Allah." dan yarinyace me shiga rai, gata da yawan fara'a. Adeel ma ya sake girma abunsa, still kuma har yanzu komai nasa Amminsa ne, Zaleeha ta zama kamar itace ta haifesa, dan komai nasa yana wajenta, akoda yaushe kuma ko unguwa zataje matuƙar basu da school to yana naniƙe da ita.
Abbi ma da Rahma suma yawanci sashin Zaleeha suke,
ba abun dake ƙara sanya su jin daɗi kaman yanda kan ƴaƴan nasu suke ahaɗe, basa taɓa kyarar juna, kowani yaro yana son ɗan uwansa. Akuma cikin shekarun da suka wuce ɗinne akayi bikin Zakariyya da amaryarsa ƴar Sarki wato Zaytoon, wanda suke ƙira da Beauty, saboda kyawunta, Zaytoon yarinyace me hankali da nutsuwa, ga kuma iya girmama nagaba da ita.

Zuwa yanzu Zakariyya da Hayatuddeen harma dasu Khamis sun tsaya akan ƙafafunsu, dan kuwa Zakariyya baiyi aure bama saida ya tabbatar da ya zama cikakken lowyer ya kama office ɗinsa na nusamman, inda koda ya tashi Aure wanda tare akayi dana Ya Habu Yaya Ahmad ne ya saya musu wasu haɗaɗɗen gida anan cikin G.R.A ɗin, basu kuma da wani nisa da gidan Baba Malam, gidajene me kyaun gaske.

Hayatudeen ma dai buri ya cika dan yanzu haka yana aiki a babban branch ɗin U.B.A Bank, wanda duk wata yake ɗiban 300k amatsayin Salary'nsa, Alhamdulillahi dan yanajin daɗin rayuwarsa, dan ba a iya aikin bankin ya tsaya ba, Hamma Saif ya ware masa dukiyarsa wanda yake na gadonsa ne, bai karɓa ba saidai yace aci gaba da juya musu kaman yanda akeyi adacan baya.
Soyayya kuwa shida Zarah sai abun da yayi gaba yayinda ita kuwa har ta fara karatu a F,C,E Zaytoon kuma na G.S.U.

Sosai Hayatuddeen ke rawan ƙafa wa bikin dan kuwa yanzu har ansaka ranan biki, ankai lefe anyi komai, ko awajen lefe baƙaramin bajinta yayi ba, dan setin akwatuna 16 yayi mata, kowanne shaƙe da kaya masu kyau da tsada, abun saidai ace masha Allah.

Khamis ma ya zama doctor yana aiki awani babban privet hospitall wanda yake mallakin Babansa ne, sai su Imran, Sulaiman, Isma'il, suma kowannensu ya kama aikinsa haiƙan, masu aikin gwamnati nayi haka ma waƴanda suka faɗa kasuwa sunayi, Abun dai saidai ace masha Allah kuma duk sunyi aure Hayatuddeen ne kaɗai ya rage.

Yau ya rage bikin Hayatuddeen saura sati ɗaya rak, inda gaba ɗaya familyɗin suke ta hidima da kuma shirye shiryen biki, sunyi anko yafi kala shida, kowa ji yake da auren na Hayatuddeen, Saifuddeen da kansa ya biyawa Hayatuddeen ɗin sadaki naira 200k,   inda kuma yasa aka sake gyaran gidan nasu, tuni dama shi ya rushe ɓangarensa ya maidashi gidan sama inda tura karshine a sama,
Adeel da Khareem Khasim Haydar da Abbi kuwa ya bar musu sashinsa na da ɗin dan yace yafi son duk motsin yaransa a kunnensa, yaran matan kuwa ko wacce tana tare da uwarta duk dama duk sunfi zama a sashin Ummee.

Kasancewar asama nan cikin sashin Ummi inda su Raleeya suka tashi, nan Hayatuddeen zai zauna da Zahrah'n sa, hakan yasa aka sake ƙawata wajen, aka sabunta komai na wajen ya zama sabo dal, ranan da akazo akayiwa Zarah'n jere kuwa ba ƙaramin kyau sashin ya ƙara ba, dan sosai iyayenta suka kashe mata kuɗi wajen saya mata tsadaddun furnitures da kuma kayan kitchine, kowa yaga jeren kuwa sai ya yaba.

Yau take laraba inda za a gudanar da haɗaɗɗiyan Kamu,  da yamma kuwa da misalin ƙarfe huɗu su Zaleeha suka tafi wajen Kamu,  bayan sun tsantsara adonsu me kyau da burgewa, Zaleeha sai sake murjewa take tana zama wata haɗaɗɗiyar mace da ita,  sam yanayin girma ko wani manyanta bai bayyana ajikinta ba, haka zalika ko mace ce ƴar uwarta ta kalleta saita kuma dan tasan Zaleeha macece iya mace, kyau, diri, sura, duk ta haɗa, hakanne yasa ko da yaushe Saifuddeen yake mutowa akanta, domin har yanzu bata sanja ba, tana nan a Zaleehanta nada, me kyawun jiki dana fuska, uwa uba zaƙi kamar zuma.

Gurin kamu fa yayi guri, an kawata ko ina dake wajen da haɗaɗɗen decoration, pink nd sky, wato kalan kayan ango da Amarya kenan,  wanda suka sha kyau har suka gaji, kallo ɗaya zaka musu kaga zallan dacewarsu da juna, tabbas hayatuddeen yayi dacen mace, dan kowa yasan Zarah yarinyace me hankali, da kuma sanyin rai, baruwanta da wasu ƴan ƙananun fitina.
Kamu yayi yanda akeso, inda su Zaleeha sukayi musu ɓarin kuɗi wajen liƙi, Raleeya ma ta taka rawar gani sosai, duk da cewa itama yanzu tana da ciki, wanda dukansa bai wuce 5 month ba, Ahmad kuwa ji yake da cikin sosai, shiyasa ma duk inda zataje yan liƙe da ita, wai bayason wani abu ya sameta.
Adda Rahama ma tazo wajen kamu'n, inda ta nunawa ɗan autan nasu gata sosai,  haka dai aka watse a kamu zuciyar kowa cike da farinciki.

Washegari Alhamis kuwa mothers day akayi, wanda Zaleeha ne da kanta ta shiryawa su Ummi, da kuma mahaifiyar Zahrah da sauran dangi, abun kuwa ya ƙawatar sosai, anci ansha sannan angaggaisa da juna,   abun dai yayi matuƙa, har akatashi zuciyar iyayen amarya da ango fari tas.
Ranan Jumma'ane da yamma aka gudanar da haɗaɗiyar Walima,  wanda acikin familyn su Saifuddeen babu wanda bai samu halasta ba, abun saidai ace masha Allah, yanayin yanda Zaleeha tayi kyau awajen Waliman ne yasa duk inda ta gilma, matan dabasu santa ba suke binta da ido.

Raihana wanda tun ana biki saura sati ɗaya tazo, zuwa yanzu babu wani rashin fahimta atsakaninta da Zaleeha'n, hasalima shiri suke sosai da sosai.
Hannun Zaleehan ta riƙo cikin salon tsokana tace.   "Matarnan kizo ki faɗamin wai miye sirrin ne, naga duk inda kikayi idanun matane ke rakaki, wato da wanka da kwalliya kike saye mana zuciyar Hamman mu ko?".
    Dariya Zaleeha tayi, tare da cewa.
"Ke zan tambaya miye sirrin ai, gashi sai haihuwa kike amma kinƙi tsufa, then har yanzu banji Saminu yana maganan ƙara aure ba."   Dariya suka sa dukansu, Raihana ne takai mata dukan wasa, cikin dariya tace.
"Wallahi dagani ba ƙari."
Haka dai aka tashi a walima bayan anyi wa'azi mai ratsa zuciya, koda suka koma gida yau Ameena itace da Saifuddeen,  duk da yasan cewar agajiye take kuwa bai ɗaga mata ƙafa ba, saida suka morewa daren na yau kafun sukayi bacci.

Washegari asabar.
Damisalin ƙarfe sha ɗaya dai-dai dubban jama'a suka shaida ɗaurin auren Hayatuddeen da kuma Zarah, wanda yasamu halartan manyan mutane da dama, dan har abokan aikin Saifuddeen saida suka halarci  ga auren.
Hayatuddeen yasha kyau abunsa cikin farar getzner,  gefensa kuwa amininsa kuma ɗan uwansa ne wato Zakariyya shiɗin ma dai yasha kyau abunsa,  gasu Imran, Khamis, Isma'il, Sulaiman, duk suma sunsha adonsu, kowannensu yana cike da farincikin auren abokin nasu.

Koda yamma tayi ƙarfe huɗu akaje aka ɗaukowa Hayatuddeen matarsa, wanda Saifuddeen da kansa yaje ɗaukowa autan Ummenshi matarsa, acikin motarsa kuwa akasaka Zarah'n. Direct gidan Ummi aka kawota, inda Ummi da kuma su aunty Mina Goggo Dada, Aunty Kubra, Umman Ishaq, sukayiwa amarya da ƴan uwanta tarba me kyau.

Karfe 8 na dare dai-dai jama'ar gidan suka fara shirin zuwa wajen diner, wanda za'a gudanar a Medugu Hall,  musamman aka ɗauko me meckup ta shirya amarya, inda ango ma yasha kyau cikin tsadaddiyar shaddansa wanda take shige da kalan kayan da  amaryarsa ta sanya.

Hamma Saif ma wata blue din getzner me tsada ya sanya, wanda tayi masa kyau sosai, hakanne yasa Zaleeha da Ameena ma sanya blue lace me kyau da tsadar gaske, wanda yake shine ankon diner'n.
Adda Rahama, Raihana, Raleeya, suma duk blue lace suka saka wanda yayi musu kyau sosai.
Haka ma abokan Hayatuddeen dukansu anko sukayi na farar shadda, da blue ɗin aiki.
Zakariyya ma farar shadda yasaka, inda Zaytoon ɗin tasa blue ɗin lace, tayi kyau itama sosai, dan kuwa tana da shigan ƙaramin ciki ajikinta.

Koda suka ƙarasa wajen diner'n, basu wani ɓata lokaci ba MC ya soma gabatar da tsare tsaren diner'n, inda yake ƙiran ƴan uwa suna nunawa ango Hayatuddeen da amaryarsa gata.

Lokacin da aka buƙaci Hamma Saif daya fito da matansa zuwa kan high table, baƙaramin ɓarin

kuɗi sukayiwa Hayatuddeen da Zarah'n ba, kuɗi suka zuba musu sosai, Hamma Saif kuwa har da dala yayiwa Hayatuddeen liƙi.
Su Adda Rahama ma sun taka rawar gani sosai awajen diner, Ahmad Ishaq, Salisu, Warisu, Saminu, Mudassir, Jabeer, Hisham ma ba abarsu abaya ba dasu da matansu ma sunyiwa autan Umme ɓarin naira.

Ƙarfe 10 dai-dai aka tashi awajen diner'n, kowa ya nufi gida, dan daga ranan bikin ya ƙare.
Koda suka dawo gida Hamma Saif kama matansa yayi suka wuce side ɗinsu.
Hayatuddeen kuwa su Zakariyya ne suka rakashi wajen amaryarsa, saida suka sayi baki kafun sukayi musu sallama, Har compound ɗin gidan Hayatuddeen ya rakosu, sam bakinsa yaƙi rufuwa, su Zakariyya sai tsiya suke masa.
Koda ya dawo ɗakin akan gado ya samu Zarah'n ta naɗe jikinta acikin mayafi, akusa da ita ya zauna tare da kamo hannunta, ya murza ƴan yatsunta, ɗayan hannunsa yasa yaɗan ɗage mayafin dake kanta, ɗago fuskarta tayi, hakan yasa suka sakarwa junansu murmushi.
Hannayensa ya buɗe alaman ta shiga jikinsa, akunyace taɗan matso kusa dashi, jawota yayi ya rungumeta atare suka sauƙe ajiyar zuciya, farinciki sukeji acikin zuciyarsu sosai da sosai cikin shauƙi Hayatuddeen ya jawo hannunta, al'wala sukaje sukayi sannan suka fito sukayi nafila kamar yadda addininmu ya koyar damu, kazar ci kici inci ya bata ta ɗanci,
kana tasha badarar daya bata daga nan ya jawota suka hau bisa gado.

Acan ɓangaren Saifudeen kuwa, acikin babban falonsa suka zauna shida matansa, kansa ya ɗaura akan cinyar Zaleeeha, yayinda ya kamo hannun Ameena dake zaune akan sofa.
Cikin ɗan gajiya Ameena ta miƙe tare da cewa.
"Saida safe".
Murmushi Zaleeha tayi tare da cewa.
"Sai da safe a ina ɗin kece da shida".
Cikin zaro ido Ameena tace.
"Wayyo Allah na rufa min asiri kin manta na fita yau ke zaki shiga rabani da wannan zala memmen mijin naki Yaƴan ko shekara ɗaya bata cikaba, gwara ke ko yanzu kika yaye Aish ta kai yaye".
A hankali ya miƙe zaune ya zuba musu idanu tare da tura baki fuska a shogoɓe yace.
"Har haka na zama marar gata guduna kukeyi, ba matsala ta uku data huɗu na bisa hanya".
Ita dai Ameena murmushi tayi ta saɓa Rahma a kafaɗa ta fita.
Shi kuwa Hamma Saif harara ya watsawa Zaleeha ya miƙe ya nufi bedroom ɗinshi alamun yayi fushi, ita kuwa Zaleeha sauƙa tayi ta nufi ɗakinta.
Nono ta bawa Aish tasha da kyau kana ta mata wonka ta mata shirin bacci ta kaita ɗakin Inna Shatu wacce yanzu a gidan take gaba ɗaya ta dawo nan sashin Zaleeha ita ke kwana da ƴan dugui-dugui ensu.

Bayan ta kaitane tayi musu saida safe,
sannan ta dawo ɗakinta tayi wonka mai rai da Ify sannan ta ƙenƙesa ado da kwaliya cikin wata azabebbiyar rigar bacci mai fitinenne ƙamshi,
kana a hankali ta nufi ɗakin Hamma Saif ɗin.

A can sashin Ummee kuwa konce take bisa gadonta kausar ƴar shekaru huɗu an shiga na biyar ne,
ke gefenta suna ƴar hirarsu ta kaka da jiki, jikarma mafi soyuwa.

Shigowan Saifudddeen ne yasa Khausar miƙewa da gudu ta faɗa jikin Hamma Saif ɗin cikin muryarta irin ta mahaifiyarta sak tace.
"Oyoyo Baby".
Da yake yana yawan kiranta Baby shiyasa itama wasu lokutan takance mishi Baby,
shafa kanta yayi tare da cewa.
"Ummee da Ummee na bakuyi bacci ba".
Murmushi Ummi tayi tare da cewa.
"Nasan zakazo kayi mana saida safe, kuma ban gankaba ai dole bazanyi bacci ga surutun Khausar, wai tana cemin in anyi Hutu zataje Abuja kuma wai fa dole tare dani zataje".
Dariya yayi cikin jin daɗi shaƙuwar Ummi da Khausar yace.
"Shike nan sai kuje tare, dan wlh Allah ko Ummi Khausar tafi sonki a kan Amminsu ma".
Dariya sukayi baki ɗaya ita kuma sai tsallenta take tayi,
suna cikin haka Zaleeha ta shigo,
bayan ta gaida Ummi ne ta ɗan kalli Khausar tare da haɗe fuska tace.
"Ke Khausar har yanzu bakiyi bacciba wato sai gobe ayita rigima dake kafin ki tafi school kiyitawa mutane kukan bacci bai isheki bako, maza wuce kije kiyi al'wala kizo ki kwanta".
Cikin sanyi tace.
"Ammi nayi al'walan".
hararan Zaleeha Saifudddeen yayi alamun meyasa zatayi mata tsawa,
cikin lallami ya shafa kan Khausar tare da cewa.
"Baby jeki konta ko".
Kai ta gyaɗa kana ta hau gado ta konta jikin Ummi,
ganin haka Hamma Saif yayiwa Umminshi saida safe kamar yadda ya saba kana ya fita ya tafi sashinsun.
hira kaɗan Zaleeha tayi da Ummi kana tabi bayanshi.

A sashin Hayatuddeen kuwa ai rawan kanshi bazai barshi ya ɗagawa Zahra ƙafaba.

A hankali take mgna cikin tsoronshi tace.
"Honey zafi nakeji".
kanshi ya cusa tsakanin wuyanta da kafaɗanta,
cikin rawan murya yace.
"My dear kiyi haƙuri, zanyi a hankali".
hannunta ta ɗan yayyarfa tare da ɗan saƙin ƙara jin yana ratsata.

A sashin Hamma Saif kuwa yana koma sade ɗinsu a falo ya zauna bisa 3 str  kana ya ɗaura system ɗinshi kan cinyarshi yana aiki.

Jin sallamar Zaleeha ne yasashi ɗan nago kanshi ido ya lumshe da sauri lokacin data cire ƙaton hijabin daya suturce tsiraitacciyar rigar baccin dake jikinta,
fuska ya haɗe tare da tura baki ya kauda kanshi waishi a dole fushi yakeyi,
murmushi tayi kana a hankali ta tako ta iso gabansa,
hannu tasa ta ɗauke system ɗinshi ta ajiyeshi kan Stull dake gefensu,
bisa cinyarshin ta zauna suna fuskantar juna da kyau, cikin tura baki yace.
"Me hakan?".
hannu tasa ta kunce igiyoyin dake sarfe gaban rigartan cikin shauƙi tace.
"Jarabace hakan, ko nayi laifin matsowa kusa da mijina ne?".
Kanshi ya kawar tare da cewa.
"Zaki karya min cinyafa".
hannunshin ta kamo ta ɗaura kan ƙirjinta tare da cewa.
"Ƙugunka nake son ka karya".
Murmushi yayi tare da cewa.
"Ashe bani kaɗai bane jarabebbe".
hannunta tasa tana zuge zip ɗin boxes shi, cikin murmushi tace.
"Ba doleba inyi jarabar wannan abun daɗin da kake bani".
murmushi yayi mai kama da dariya, yace.
"Yau aikin nakine to in kina son in huce".
da sauri tasa hannu ta kamo nashi ta mannashi kan mararta tare da cewa.
"Dama fushi kakeyi dani ne?".
Kanshi ya jujjuya mata kamar ƙaramin yaro ko gaula hannunshi ya ƙara manna da mararta jin yadda taketa tsiyaya cikin sakartacciyar murya a hankali yace.
"Aaa a, bana fushi dake mai lamɓun daɗeeeeee".
ido ta ɗan zaro jiyo sautin muryar Zahran Hayatuddeen can ƙasa tana kuka.

Su kuwa duk da yadda Hayatuddeen ke binta a hankali yayin amsar budurcin saida tayi kukan zafin da ba'a rasaba,
cikin muryar kuka autan Ummen daya jishi a duniyar da bai taɓa shigaba yake cewa.
"Wayyo daɗi daɗi daɗi wayyo Ummina yau kam autanki ya girma".
ya ƙarishe mgnar da ɗan karfi, kasan cewar a sama suke kuma suma su Hamma Saif a sama suke kuma basuyi bacciba hakanne yasa sukaji duk surutan Autan Ummi.

Ita kuwa Ummi da Khausar tuni sunyi baccinsu.

Dariya Hamma Saif yayi tare da cewa.
"Wayyo My happiness nima bani kayan daɗi, kinji autan Umme can yaji kayan daɗi".
hannu Zaleeha tasa tana zare kayan jikinshi kana shima yana cire mata fingilar rigar jikinta, cikin wata sassanyan murya Zaleeha tace.
"Zan baka kayan daɗinki Hamma Saif ɗina,Zaujil al'muazzam, in sha Allah ni takace har gaban Abadan, na godewa Allah da nayi halin ƳAR FULANI, domin da nayi sakaci da addu'a nabi zugar muguwar ƙawa da MI,WASMITI, NAYI NADAWA a tsawo rayuwata da ban dawo gidanka ba ƙarƙashin inuwar aure, da nayi babban asarar kamilin mijin tabbas na yardae NAMIJI BAYA

KAƊAN dan da nabi shawarar ɗan ƙaramin ƙanina Zakariyya da ban guduba,   da a hankali zan gane kaine nake nema mutumin da ya zame min jigon A TAUSAYAWA JUNA, ya zame min BANDIRAWO, a lokacin da na rasa mai taimako a a hannun mugu Dalla, koda yake na gane cewa RUBUTACCEN AL'AMARI shiyasa na gudu dan rabon Ummu Adeel da yaranta, guduwata yasa naiwa kaina kishiya, saida sanadin RIGAR KOWA mutuwa data ɗauke min Adda Maryam ta zama sanadin dawowata gidan mijina cikin HUKUMCIN ALLAH gashi ka zama uban ƴaƴana, kuma, tabbas na shaida zan kuma gayawa duniya wallahi tallahi NAKASA BA KASAWA BACE, dan wani nasasshenma yafi lafiyayyan na miji iya sarrafa mace,
Ni dai ka zame min babban GARKUWA  a rayuwar duniya da ƙiyama in sha Allah". Tana gama ya miƙe tsam ruggumeda ita bedroom suka shiga suna shiga ya kontar da ita bisa gado da sauri ya dawo bakin ƙofa cikin sanyi yace.
"Bari in rufe mana ƙofa kada AYSHA ALIYU GARKUWA ta shigo ta samu abin rubutawa fans ɗinta masu son ganin gindin biro, to mu dai a rabu damu, masoyan AYSHA ALIYU GARKUWA ku bita a sabon littafinta da zatayi muku mai suna *GARKUWA*".
Daga nan ya rufe ƙofar ta yadda ban samu damar gani ko jin komaiba.

ALHAMDULILLAH! ALHAMDULILLAH!! ALHAMDULILLAH!!!

Na godewa Allah daya bani damar gama littafin nan lfy kamar yadda na farashi lfy,
Sai kuma in mun sake haɗuwa a sabon littafina mai suna GARKUWA wanda in sha Allah daga gobe zan fara typing, amman nida fara posting bansa rana ba, sai ranar da Allah ya nufa, dan zanke typing ɗin ne ina kuma hutawa.

Godiya ta musamman a gareku masoyana masoyan littatafaina.

Fatan al'khairi a gareku da ɗumbin godiya Dija chiroma, Mom Asas, Rafi'a, Maman Hajia, Ina godiya da hidimar yiwa sabbin members posting a duk sanda suka nema ngd matuƙa Allah ya bar zumunci da qauna ya raya mana ahlinmu bisa imani.

Afwan! Afwan!! Afwan!!! da wanda suka biya da wanda suka karanta na sata mace ko namiji babba ko yaro wanda na sani da wacce ban saniba wacce muka taɓa mgna da ita da wacce ban taɓa magana da itaba ku yafe min in akwai wanda na ɓatawa rai kona sosawa zuƙata a bisa rashin sani da ajizanci na ɗan Adam, ina fatan Allah ya ƙaddara saduwarmu a sabon littafina, in kuma rai yayi halinshi ku yafe min Allah ya ƙaddara saduwarmu a darassalam.

Godiya da jinjina a gareki Mommy Niger ngd Ngd Ngd Matuƙa da kekyawar niyarki da karramawarki gareni da sona da arziki da kikayi Alhamdulillah kuɗin waɗanda suka sayi littafi na Niger sun isoni lfy tare da taimakon ƙanwata Ummi Garkuwa ngd matuƙa da karamawarku.

Jinjina gareka Umar MB ngd da Jingel Allah ya ƙaro basirar waƙa.

Gaisuwa mai tarin yawa ga dukkan nakasassun duniya baki ɗaya, GARKUWAR NAKASASSU tanai muku fatan al'khairi.

Fatima Sardauna Ina godiya mai tarin yawa a gareki, Allah ya bar zumunci da qauna. Allah ya azirtaki da zuriya ta gari.  Allah ya ƙara danƙon so da surkina.

LITTAFIN GARKUWA LITTAFIN  MAI CIKE DA SARKAƘIYA DA Hargitsi al'ajabi tausayi sassanyan salo mai ratsa zuciya ZAZZAFAN SOYAYYA ƘASAITACCEN ƊAN GWAMNA JIKAN SARKI YOLA KANA JIKAN SARKIN MUSULMAI TSATSON MASARAUTAR SAUDIYA, KAMILIN MALAMI DOCTOR KANA DA KUMA WASU SIRRIKA MASU TAKE BAKAN GIZO, amman duk da haka yana cikin yanayin mai ban tausayi ga duk wani mai imani duk da ƙarfin zuciya da imani dake zuciya da jikinshi yana kauda komai duk duniya mutun ukune rak suka san matsalarsa, to wai meyake damun rayuwarsa duk da tarin gada nasaba mulki sarauta soyayyan iyaye da kakanni, meyasa baya dariya? Meyasa bai yarda da kowaba? Me ke damun rayuwarsa? Ta ina warakarsa take? Menene babban burinshi?.
Ya kasance shine GARKUWAN FULANIN ƘASAR NAN BAKI ƊAYA yana adalin shugabane wane halacci Fulanin ruga sukeyi mishi?
ƳAR MAKIYAYA NE FULANIN RUGA MUTUNCE ITA KOKO Aljan TO AMMAN IDANUNTA BA BIYU BANe kamar na koma a fuska dai idanun biyu ne tofa amman TANA IYA GANIN ABINDA BA KOWA KE GANIBA ITACE GARKUWARSA ITA KE KUNCE DUK ƘULLIN DA AKE MISHI da tone duk abinda aka binnewa rayuwarsa. SHI KUWA MISHKILINE MAI BAN MAMAKI BAI YARDA DA KOWABA A DUNIYA SAI MUTUN UKU RAK MAHAKIRUNCINE MAI IYA KAUDA KAI TO WAI MEYA RASA A RAYUWARSA NE BAYA MAGANA SAI TA KAMA DOLE BAYA DARIYA SAI DAI BAKINSA BAYA RABUWA DA FURTA WASU MALAMAI WANDA SUN ZAME MASA ABINCI DA abin SHA, ANSA ƘANNENSHI A LAYI MAI WUYA KANA AN ZAUTAR DA BABBAN YAYANSHI YA ZAMA DOLE ShiNE GARKUWARSU DUKANSU, YANA BUKATAR MAKUSANCI TO WAI MENENE SANADI UHUM DAGA TAIMAKO.... UHUMMM ABIN BAZAI FAƊUBA, WLH NI DAI A KARAN KAINA BAN TAƁA YIN LITTAFIN DA NAKE JIN DADINSHIBA KAMAR GARKUWA, Ibrin yana sani shauƙi shiyasa ma bazanyi wani hutuba zan fara typing sabida na ɗokantu dashi.

Ko ta  ina na labarin abin sone yanada salo mai ratsa zuciya ni ɗaya nakanyi ta murmushi in ina kitsima Ibrin🤝🏻🤝🏻🤝🏻🥰😘

Fatan al'khairi masoyana Sai mun haɗu a GARKUWA.

By
*GARKUWAR FULANI*